الحزب ٣٩ ۞ فَمَا كَانَ جَوَابَ قَوْمِهِۦٓ إِلَّآ أَن قَالُوٓاْ أَخْرِجُوٓاْ ءَالَ
لُوطٍ مِّن قَرْيَتِكُمْ ۖ إِنَّهُمْ أُنَاسٌ يَتَطَهَّرُونَ ٥٦ فَأَنجَيْنَٰهُ
وَأَهْلَهُۥٓ إِلَّا ٱمْرَأَتَهُۥ قَدَّرْنَٰهَا مِنَ ٱلْغَٰبِرِينَ ٥٧ وَأَمْطَرْنَا
عَلَيْهِم مَّطَرًا ۖ فَسَآءَ مَطَرُ ٱلْمُنذَرِينَ ٥٨ قُلِ ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ
وَسَلَٰمٌ عَلَىٰ عِبَادِهِ ٱلَّذِينَ ٱصْطَفَىٰٓ ۗ ءَآللَّهُ خَيْرٌ أَمَّا يُشْرِكُونَ
٥٩ أَمَّنْ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ وَأَنزَلَ لَكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ
مَآءً فَأَنۢبَتْنَا بِهِۦ حَدَآئِقَ ذَاتَ بَهْجَةٍ مَّا كَانَ لَكُمْ أَن
تُنۢبِتُواْ شَجَرَهَآ ۗ أَءِلَٰهٌ مَّعَ ٱللَّهِ ۚ بَلْ هُمْ قَوْمٌ يَعْدِلُونَ ٦٠
أَمَّن جَعَلَ ٱلْأَرْضَ قَرَارًا وَجَعَلَ خِلَٰلَهَآ أَنْهَٰرًا وَجَعَلَ
لَهَا رَوَٰسِىَ وَجَعَلَ بَيْنَ ٱلْبَحْرَيْنِ حَاجِزًا ۗ أَءِلَٰهٌ مَّعَ ٱللَّهِ ۚ
بَلْ أَكْثَرُهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ٦١ أَمَّن يُجِيبُ ٱلْمُضْطَرَّ إِذَا
دَعَاهُ وَيَكْشِفُ ٱلسُّوٓءَ وَيَجْعَلُكُمْ خُلَفَآءَ ٱلْأَرْضِ ۗ
أَءِلَٰهٌ مَّعَ ٱللَّهِ ۚ قَلِيلًا مَّا تَذَكَّرُونَ ٦٢ أَمَّن يَهْدِيكُمْ فِى
ظُلُمَٰتِ ٱلْبَرِّ وَٱلْبَحْرِ وَمَن يُرْسِلُ ٱلرِّيَٰحَ بُشْرًۢا بَيْنَ يَدَىْ
رَحْمَتِهِۦٓ ۗ أَءِلَٰهٌ مَّعَ ٱللَّهِ ۚ تَعَٰلَى ٱللَّهُ عَمَّا يُشْرِكُونَ ٦٣



**(56) Mutanensa basu samu wata amsa da za su ba shi ba, face faxinsu: “Ku fitar da mabiya Luxu daga Alqaryarku. Su mutane ne da suke tsarkaka daga qazanta da najasa”. Sun faxi haka ne suna masu izgili ga mabiya Annabi Luxu, waxanda basa tarayya da su wajen aikata alfasha, asali ma hana su aikatawa suke yi.**

**(57) Sai muka quvutar da shi da iyalansa, ban da matar shi, mun hukunta ta kasance cikin masu wanzuwa cikin azaba, don ta zama cikin halakakku.**

**(58) Muka yi musu ruwan duwatsu daga sama, sai ya kasance ruwan sama ne mummuna, mai halakarwa ga waxanda aka tsorata su da azaba, amma ba su amsa kira ba.**

**(59) Ka ce – Ya kai wannan Manzo -: “Godiya ta tabbata ga Allah a kan ni’imominsa, da amincin da ya yi wa sahabban Annabi (S.A.W) daga azabarsa, wadda ya azabta mutanen Annabi Luxu da Salihu da ita”. Shin Allah wanda shi ne abin bauta da cancanta, kuma mulkin komai yake hannunsa shi ne mafi alheri, ko kuwa abubuwan da Mushirikai suke bautawa, waxanda basa mallakar wani amfani ko cutarwa?!.**

**(60) Ko shin wanda ya halicci sammai da qassai ba tare da wani samfuri da ya gabata ba, kuma ya saukar muku ruwa daga sama – Ya ku mutane-, muka tsirar muku gonaki masu kyau da qayatarwa, irin waxanda ba zaku iya fitar da irin waxannan bishiyoyin a waxannan gonaki ba, saboda gajiyawar ku a kan yin hakan. Allah shi ne ya fitar da su. Shin akwai wani abin bauta da ya yi wannan tare da Allah?!. A’a, babu! Kawai dai su mutane ne, da suke karkacewa gaskiya, sai su daidaita Mahalicci da abubuwan halitta don zalunci.**

**(61) Ko kuma shin wanda ya mayar da qasa matabbata, tsayayya, ba ta zamewa da waxanda suke a bayanta, kuma ya saka qoramu masu gudana a cikinta, kuma ya saka mata duwatsu tabbatattu, kuma ya saka shamaki tsakanin tekuna guda biyu, na gishiri da mai daxi, wanda yake hana cakuxuwar ruwan gishirin da mai daxi, don kada ya vata shi, ya zama maras daxin sha. Shin akwai wani abin bauta da ya yi wannan tare da Allah?! A’a, babu! Kawai dai mafi yawansu basu sani ba, don da sun sani, da basu haxa Allah da wani daga cikin halittarsa ba wajen bauta.**

**(62) Kuma wane ne wanda ya ke amsa kiran wanda lamarinsa ya yi masa qunci, ya shiga cikin tsanani, idan ya kira shi, kuma yake xauke wa mutum abin da yake faruwa da shi na cuta da talauci da sauransu, kuma yake mayar da ku mamaya juna a bayan qasa, sashenku yana maye gurbin sashe, jama’a bayan jama’a? Shin akwai wani abin bauta ne tare da Allah da yake aikata haka?!. A'a, babu! Kaxan ne daga cikinku suke wa’azantuwa da xaukan izina.**

**(63) Kuma wa yake shiryar da ku a cikin duhu, a kan tudu da teku, ta hanyar abubuwan da ya kafa muku na alamu da taurari, kuma wa yake aiko iska xauke da albishir na kusantowar saukar ruwan sama, wanda yake jin qan bayinsa da shi. Shin akwai wani abin bauta ne da yake yin haka tare da Allah?! Tsarki ya tabbata ga Allah daga barin abin da suke masa tarayya da shi cikin halittunsa!.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Bayanin yadda mavarnata suke komawa tashin hankali, yayin da hujjojin gaskiya suka kewaye su.**
**2 - Dangatakar auratayya ba tare da imani ba, bata amfani a lahira.**
**3 - Tabbatar da aqidar tauhidi, ta hanyar tunatarwa da ni'imomin Allah.**
**4 - Duk wani wanda ke cikin matsatsi, mumini ne ko kafiri, to Allah ya yi masa alqawarin zai amsa masa, idan ya roqe Shi.**

أَمَّن يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ وَمَن يَرۡزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِۗ
أَءِلَٰهٞ مَّعَ ٱللَّهِۚ قُلۡ هَاتُواْ بُرۡهَٰنَكُمۡ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٦٤ قُل
لَّا يَعۡلَمُ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ ٱلۡغَيۡبَ إِلَّا ٱللَّهُۚ وَمَا يَشۡعُرُونَ
أَيَّانَ يُبۡعَثُونَ ٦٥ بَلِ ٱدَّٰرَكَ عِلۡمُهُمۡ فِي ٱلۡأٓخِرَةِۚ بَلۡ هُمۡ فِي
شَكّٖ مِّنۡهَاۖ بَلۡ هُم مِّنۡهَا عَمُونَ ٦٦ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَءِذَا
كُنَّا تُرَٰبٗا وَءَابَآؤُنَآ أَئِنَّا لَمُخۡرَجُونَ ٦٧ لَقَدۡ وُعِدۡنَا هَٰذَا
نَحۡنُ وَءَابَآؤُنَا مِن قَبۡلُ إِنۡ هَٰذَآ إِلَّآ أَسَٰطِيرُ ٱلۡأَوَّلِينَ ٦٨
قُلۡ سِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَٱنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُجۡرِمِينَ
٦٩ وَلَا تَحۡزَنۡ عَلَيۡهِمۡ وَلَا تَكُن فِي ضَيۡقٖ مِّمَّا يَمۡكُرُونَ ٧٠
وَيَقُولُونَ مَتَىٰ هَٰذَا ٱلۡوَعۡدُ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٧١ قُلۡ عَسَىٰٓ
أَن يَكُونَ رَدِفَ لَكُم بَعۡضُ ٱلَّذِي تَسۡتَعۡجِلُونَ ٧٢ وَإِنَّ رَبَّكَ
لَذُو فَضۡلٍ عَلَى ٱلنَّاسِ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَهُمۡ لَا يَشۡكُرُونَ ٧٣ وَإِنَّ
رَبَّكَ لَيَعۡلَمُ مَا تُكِنُّ صُدُورُهُمۡ وَمَا يُعۡلِنُونَ ٧٤ وَمَا مِنۡ غَآئِبَةٖ
فِي ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِ إِلَّا فِي كِتَٰبٖ مُّبِينٍ ٧٥ إِنَّ هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانَ
يَقُصُّ عَلَىٰ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ أَكۡثَرَ ٱلَّذِي هُمۡ فِيهِ يَخۡتَلِفُونَ ٧٦



**64 Wa yake fara halitta a cikin mahaifa, zango bayan zango, sannan ya rayar da shi bayan ya kashe shi, kuma wa yake azurta ku daga sama da ruwan da yake saukar da shi daga vangarensa, kuma yake azurta ku daga qasa da tsirran da yake fitar da su daga cikin ta. Shin akwai wani abin bauta tare da Allah da yake aikata haka?!. Ya kai wannan Manzo, ka ce wa waxannan Mushirikai: "Ku kawo hujjojinku a kan abin da kuke kai na shirka, in kuna da gaskiya cikin abin da kuke iqrarinsa na ce wa kuna kan gaskiya".**

**65 Ka ce - Ya kai wannan Manzo-: "Babu wani wanda ke cikin sammai na Mala'iku, ko wanda yake bayan qasa na mutane, da ya san gaibu, sai Allah shi kaxai, shi ne wanda ya san gaibu. Haka kuma dukkan waxanda suke sammai da qassai, babu wanda ya san ranar da za a tayar da su, don yin sakamako sai Allah.**

**66 Ko iliminsu ya miqe har zuwa ga sanin lahira ne, ta yadda har suka yi yaqini da ita?. A'a, kawai suna cikin shakku ne da ruxu dangane da lahira. Kai! tabbas basirar su ta makance dangane da ita.**

**67 Waxanda suka kafirta suka ce - suna masu inkari -: "Shin yanzu idan mun mutu, mun zama turvaya, kuma za a sake tayar da mu rayayyu?".**

**68 Haqiqa an yi mana alqawari, kuma an yi wa iyayenmu alqawari gabanin mu, cewa za a tayar da mu baki xaya, amma har yanzu bamu ga tabbacin wannan alqawari ba. Don haka wannan alqawarin da aka yi mana, gaba xayansa ba komai ba ne face qarerakin mutanen farko, waxanda suka rubuta su a littafansu.**

**69 Ya kai wannan Manzo, ka faxa wa waxannan masu qaryata tashi bayan mutuwa, cewa: "Ku yi tafiya a kowane vangare a bayan qasa, ku lura yaya qarshen masu laifi, masu qaryata tashi bayan mutuwa ya kasance. Lallai mun halaka su, saboda qaryatawarsu ga tashi bayan mutuwa.**

**70 Kar ka yi baqin ciki saboda kawar da kan mushirikai daga da'awar ka, kuma kada qirjinka ya yi qunci saboda makircinsu, Allah zai baka nasara a kansu.**

**71 Kafirai masu inkarin tashi bayan mutuwa cikin mutanenka suna cewa: "Yaushe ne abin da kake mana**
**alqawarinsa kai da muminai na azaba zai tabbata, in kuna da gaskiya cikin abin da kuke iqrari na faruwar**
**hakan?!". 72 Ka ce da su – Ya kai wannan Manzo-: "Ta yi wu abin da kuke nemansa da gaggawa na azaba ya kusa**
**ya zo muku".**

**73 Kuma lallai Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo-: "Ma'abocin falala ne a kan mutane, ta yadda yake barin gaggauto musu da azaba, duk da abin da suke kai na kafirci da savo, sai dai mafiya yawan mutane basa godewa Allah a kan abin da yake yi musu ni'ima da shi".**

**74 Kuma lallai Ubangijinka yana sane da abin da zukatan bayi suke voyewa, da abin da suke bayyanawa, babu wani abin da yake vuya a gare shi, kuma da sannu zai yi musu sakayya a kai.**

**75 Babu wani abu wanda yake vuya ga mutane a sama ko a qasa, face yana cikin wani littafi mabayyani, wanda shi ne lauhul-Mahfuz.**

**76 Haqiqa wannan Alqur'ani da aka saukar wa Annabi Muhammad (S.A.W) yana labarta wa bani Isra'ila mafi yawan abin da suke savani a cikinsa, kuma yana bayyana karkacewarsu.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Sanin gaibu yana daga cikin abubuwan da Allah ya kevanta da su, don haka yin iqrarinsa kafirci ne.**

**2 - Yin la'akari da al'ummun da suka gabata, ta fuskar makomarsu da halayensu, hanya ce ta tsira.**

**3 - Kewayewar ilimin Allah da ayyukan bayinsa. 4 - Bayanin yadda Alqur'ani yake yi wa Bani Isr'aila gyara, a cikin abin da suka karkace, da abin da suka canza daga littafansu.**

وَإِنَّهُۥ لَهُدٗى وَرَحۡمَةٞ لِّلۡمُؤۡمِنِينَ ٧٧ إِنَّ رَبَّكَ يَقۡضِي بَيۡنَهُم
بِحُكۡمِهِۦۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡعَلِيمُ ٧٨ فَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِۖ إِنَّكَ عَلَى
ٱلۡحَقِّ ٱلۡمُبِينِ ٧٩ إِنَّكَ لَا تُسۡمِعُ ٱلۡمَوۡتَىٰ وَلَا تُسۡمِعُ ٱلصُّمَّ ٱلدُّعَآءَ
إِذَا وَلَّوۡاْ مُدۡبِرِينَ ٨٠ وَمَآ أَنتَ بِهَٰدِي ٱلۡعُمۡيِ عَن ضَلَٰلَتِهِمۡۖ إِن
الحِزۡبُ ٣٩ تُسۡمِعُ إِلَّا مَن يُؤۡمِنُ بِـَٔايَٰتِنَا فَهُم مُّسۡلِمُونَ ٨١ ۞ وَإِذَا وَقَعَ
ٱلۡقَوۡلُ عَلَيۡهِمۡ أَخۡرَجۡنَا لَهُمۡ دَآبَّةٗ مِّنَ ٱلۡأَرۡضِ تُكَلِّمُهُمۡ أَنَّ
ٱلنَّاسَ كَانُواْ بِـَٔايَٰتِنَا لَا يُوقِنُونَ ٨٢ وَيَوۡمَ نَحۡشُرُ مِن كُلِّ أُمَّةٖ
فَوۡجٗا مِّمَّن يُكَذِّبُ بِـَٔايَٰتِنَا فَهُمۡ يُوزَعُونَ ٨٣ حَتَّىٰٓ إِذَا جَآءُو قَالَ
أَكَذَّبۡتُم بِـَٔايَٰتِي وَلَمۡ تُحِيطُواْ بِهَا عِلۡمًا أَمَّاذَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ
٨٤ وَوَقَعَ ٱلۡقَوۡلُ عَلَيۡهِم بِمَا ظَلَمُواْ فَهُمۡ لَا يَنطِقُونَ ٨٥ أَلَمۡ
يَرَوۡاْ أَنَّا جَعَلۡنَا ٱلَّيۡلَ لِيَسۡكُنُواْ فِيهِ وَٱلنَّهَارَ مُبۡصِرًاۚ إِنَّ فِي
ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ ٨٦ وَيَوۡمَ يُنفَخُ فِي ٱلصُّورِ فَفَزِعَ مَن
فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَن فِي ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا مَن شَآءَ ٱللَّهُۚ وَكُلٌّ أَتَوۡهُ
دَٰخِرِينَ ٨٧ وَتَرَى ٱلۡجِبَالَ تَحۡسَبُهَا جَامِدَةٗ وَهِيَ تَمُرُّ مَرَّ ٱلسَّحَابِۚ
صُنۡعَ ٱللَّهِ ٱلَّذِيٓ أَتۡقَنَ كُلَّ شَيۡءٍۚ إِنَّهُۥ خَبِيرُۢ بِمَا تَفۡعَلُونَ ٨٨



**(77) Kuma haqiqa shi (Alqur’ani) shiriya ne da jin qai ga masu aiki da abin da ya zo a cikinsa.**

**(78) Haqiqa Ubangijinka - Ya kai wannan Manzo- shi ne zai yanke hukunci tsakanin mutane, Muminansu da Kafiransu a ranar alqiyama, da hukuncinsa na adalci, sai ya jiqan muminai, ya azabtar da kafirai. Kuma shi ne Mabuwayi, wanda yake xaukan fansa a kan maqiyansa, babu mai galaba a kansa, kuma masani, wanda mai gaskiya da mai qarya ba sa shige masa duhu.**

**(79) Don haka ka dogara ga Allah a cikin dukkanin al'amuranka. Lallai kana kan gaskiya mabayyaniya. (80) Haqiqa kai – Ya wannan Manzo- ba ka jiyar da matattu, waxanda zukatansu sun mutu, saboda kafirce wa Allah, kuma baka jiyar da marasa ji (kurame) abin da kake kiransu zuwa gare shi, idan suka koma suna masu juya maka baya. (81) Kai ba mai iya shiryar da waxanda basirarsu ta makance daga ganin gaskiya ba ne, don haka kar ka yi baqin cikin a kansu, ka wahalar da kanka. Ba zaka iya jiyar da da'awarka ba, face sai ga waxanda suka yi imani da ayoyinmu, su masu miqa wuya ne ga umarnin Allah.**

**(82) Kuma idan azabata ta wajaba, kuma ta tabbata a kansu, saboda dogewarsu a kan kafirci da savonsu, ashararan mutane suka rage, to zamu fitar musu da wata babbar alamar tashin alqiyama, idan ta kusa, ita ce wata dabba daga qasa, wadda zata yi musu magana da abin da suke fahimta cewa: Lallai mutane sun kasance dangane da ayoyinmu da muka saukar da su ga Annabinmu ba masu gasgatawa ba ne. (83) Ya kai wannan Manzo, ka ambaci ranar da zamu tayar, daga kowace al'umma, wasu jama’a daga cikin manyansu, waxanda suka qaryata ayoyinmu, za a haxa na farkonsu da na qarshensu, sannan sai a kora su zuwa ga hisabi. (84) Za a ci gaba da kora su, har sai sun zo wurin da za a yi musu hisabi, sai Allah ya ce da su, yana mai wulaqanta su: “Wato kun qaryata ayoyina, waxanda suke nuna kaxaitaka ta, kuma suka qunshi shari'o'i na, ba tare da kun samu cikakken sanin cewa vatattu ne, da ya halatta ku qaryata su ba, ko ku san me ya kamata ku aikata dangane da su, gasgatawa ko qaryatawa?!. (85) Azaba ta afku a kansu saboda zaluncinsu, da kafirce wa Allah, da qaryata ayoyinsa, saboda haka ba zasu iya wata magana ta kare kansu ba, saboda gazawarsu da lalacewar hujjojinsu. Yayin da ya kasance suna kore yiwuwar tashi bayan mutuwa, sai Allah ya faxakar da su da abin da yake nuna yiwuwar hakan a rayuwarsu, shi ne barcin da suke yi, wanda yake a matsayin mutuwa, da farkawarsu, wadda take a matsayin tashi bayan mutuwa, ya ce: (86) Shin waxannan masu qaryata tashi bayan mutuwa, basa ganin yadda muka sanya dare, don su huta a cikinsa da barci, kuma muka sanya yini mai haske, don su ga juna a cikinsa, su tafi zuwa ga ayyukan su. Lallai a cikin wannan mutuwa mai maituwa da tayarwa bayanta akwai alamu bayyanannu ga mutane masu imani. (87) Ya kai wannan Manzo - ka ambaci ranar da Mala'ikan da aka wakilta shi da busa zai yi busa ta biyu a cikin qaho, sai dukkan wanda yake cikin sammai da qassai ya firgita, sai waxanda Allah ya togace su daga firgita, saboda falalarsa. Kuma dukkanin halittun Allah zasu zo masa a wannan ranar suna masu biyayya da qanqan da kai. (88) Zaka ga duwatsu a wannan ranar, kana zatonsu tabbatattu ne a wuri xaya, basa motsi, alhali kuwa suna tafiya da sauri, irin saurin girgije. Halittar Allah kenan. Shi ne wanda yake motsar da ita, tana tafiya. Haqiqa Allah masani ne mai bada labari ga abin da kuke aikatawa. Babu wani abu na aikinku da yake vuya a gare shi. Kuma da sannu zai yi muku sakayya a kai.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Muhimmancin dogaro da Allah. 2 - Tsarkake Annabi Muhammad (S.A.W) da cewa yana kan gaskiya mabayyaniya. 3 - Shiriya ta dacewa a hannun Allah take, ba a hannun Manzon Allah (S.A.W) ba. 4 - Bayanin yadda barci yake nuna mutuwa, kamar yadda tashi daga barci yake nuna tashi bayan mutuwa.**

مَن جَآءَ بِٱلۡحَسَنَةِ فَلَهُۥ خَيۡرٞ مِّنۡهَا وَهُم مِّن فَزَعٖ يَوۡمَئِذٍ ءَامِنُونَ ٨٩
وَمَن جَآءَ بِٱلسَّيِّئَةِ فَكُبَّتۡ وُجُوهُهُمۡ فِي ٱلنَّارِ هَلۡ تُجۡزَوۡنَ إِلَّا
مَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٩٠ إِنَّمَآ أُمِرۡتُ أَنۡ أَعۡبُدَ رَبَّ هَٰذِهِ ٱلۡبَلۡدَةِ
ٱلَّذِي حَرَّمَهَا وَلَهُۥ كُلُّ شَيۡءٖۖ وَأُمِرۡتُ أَنۡ أَكُونَ مِنَ ٱلۡمُسۡلِمِينَ
٩١ وَأَنۡ أَتۡلُوَاْ ٱلۡقُرۡءَانَۖ فَمَنِ ٱهۡتَدَىٰ فَإِنَّمَا يَهۡتَدِي لِنَفۡسِهِۦۖ
وَمَن ضَلَّ فَقُلۡ إِنَّمَآ أَنَا۠ مِنَ ٱلۡمُنذِرِينَ ٩٢ وَقُلِ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ
سَيُرِيكُمۡ ءَايَٰتِهِۦ فَتَعۡرِفُونَهَاۚ وَمَا رَبُّكَ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعۡمَلُونَ ٩٣

سُورَةُ القَصَصِ — ترتيبها ٢٨ — آياتها ٨٨

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

طسٓمٓ ١ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱلۡكِتَٰبِ ٱلۡمُبِينِ ٢ نَتۡلُواْ عَلَيۡكَ
مِن نَّبَإِ مُوسَىٰ وَفِرۡعَوۡنَ بِٱلۡحَقِّ لِقَوۡمٖ يُؤۡمِنُونَ ٣ إِنَّ
فِرۡعَوۡنَ عَلَا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَجَعَلَ أَهۡلَهَا شِيَعٗا يَسۡتَضۡعِفُ
طَآئِفَةٗ مِّنۡهُمۡ يُذَبِّحُ أَبۡنَآءَهُمۡ وَيَسۡتَحۡيِۦ نِسَآءَهُمۡۚ إِنَّهُۥ كَانَ
مِنَ ٱلۡمُفۡسِدِينَ ٤ وَنُرِيدُ أَن نَّمُنَّ عَلَى ٱلَّذِينَ ٱسۡتُضۡعِفُواْ
فِي ٱلۡأَرۡضِ وَنَجۡعَلَهُمۡ أَئِمَّةٗ وَنَجۡعَلَهُمُ ٱلۡوَٰرِثِينَ ٥



**(89) Duk wanda ya zo ranar alqiyama da imani da kyakkyawan aiki, to yana da Aljanna. Kuma waxannnan su ne amintattu da amincin Allah daga razanar ranar alqiyama.**
**(90) Wanda kuwa ya zo da kafirci da savo, to suna da wuta, za a jefa su a cikinta a kan fuskokinsu, kuma za a ce musu - cikin tsawatarwa da wulaqanci -: "Shin ana saka muku da wani abu ne, face da abin da kuka kasance kuna aikatawa a duniya, na kafirci da savo?!".**
**(91) Ka ce da su - Ya kai wannan Manzo-: "Kaxai dai an Umarce ni in bautawa Ubangijin Makka wanda ya haramta ta, ba a zubar da jini a cikinta, ba a zaluntar kowa a cikinta, ba a kashen abin farautar ta, ba a yanke bishiyoyinta. Kuma Allah (S.W.T) shi yake da mulkin komai. an umarce ni in kasance cikin masu miqa wuya ga Allah, da qanqan da kai a gare shi da xa'a".**
**(92) Kuma an umurce ni in karantawa mutane Alqaur'ani, duk wanda ya shiryu da shiriyarsa, ya yi aiki da abin da yake cikinsa, to amfanin shiriyar da ya yi, don kansa ne. Wanda kuwa ya karkace ya vace daga shiriyarsa, ya yi inkarinsa, ya qi yin aiki da abin da yake cikinsa, to ka ce: "Kaxai ni ina cikin masu gargaxi ne, ina muku gargaxi daga azabar Allah, amma shiriyar ku ba a hannu na take ba".**
**(93) Ya kai wannan Manzo- ka ce: "Godiya ta tabbata ga Allah a kan ni'imominsa, waxanda baza su qidayu ba. Da sannu Allah zai nuna muku ayoyinsa a cikin kawunanku, da cikin sammai da qassai da arziki, ku san su, sanin da zai shiryar da ku zuwa ga miqa wuya ga gaskiya. Kuma Ubangijinka ba mai rafkanuwa ba ne dangane da abin da kuke aikatawa, yana ganin su, babu abin da yake vuya a gare shi, kuma da sannu zai yi muku sakayya a kai.**

# Suratul Qasas

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Ambaton ma'aunan qarfi na haqiqa, ta hanyar bayyana ikon Allah da sunnarsa ta bayar da nasara ga raunana, da halakar da masu girman kai**

**Tafsir:**

**(1) (Xaa Sin Mim): Bayani ya gabata dangane da ire-iren waxannan haruffa a farkon Suratul Baqara.**
**(2) Waxannan ayoyin Alqur'ani bayyananne ne. (3) Muna karanta maka labarin Annabi Musa da Fir'auna da gaskiyar da babu shakka a cikinta ga mutanen da suke yin imani, saboda su ne masu amfana da abin da yake cikinsa. (4) Haqiqa Fir'auna ya yi shisshigi a qasar Misra, ya mamaye ta, ya mayar da mutanen ta qungiya qungiya, ya raba tsakaninsu, yana raunana wani vangare daga cikinsu, su ne vangaren Bani Isra'ila, ta hanyar kashe 'ya'yansu maza, da barin 'ya'yansu mata da rai, don yin hidima, da matuqa wajen qasqantar da su. Haqiqa ya kasance cikin mavarnata a bayan qasa, ta hanyar zalunci da wuce gona da iri, da girman kai. (5) Muna so mu yi ni'ima a kan Bani Isra'ila, waxanda Fir'auna ya raunana su a garin Misra, ta hanyar halaka maqiyansu, da kawar da rauni daga gare su, da mayar da su jagorori, waxanda za a riqa koyi da su cikin gaskiya, kuma mu sanya su su gaji qasar Sham mai albarka, bayan halakar da Fir'auna, kamar yadda Allah ya ce: (Muka gadar wa mutanen da aka kasance ana raunana su gabashin qasa da yammacinta, wadda muka sa albarka a cikinta...).**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Imani da aiki nagari sababi ne na tsira daga firgici a ranar alqiyama. 2 - Kafirci da savo sababi ne na shiga wuta. 3 - Haramta kisa da zalunci da farauta a harami. 4 - Nasara da tabbata su ne qarshen al'amarin Muminai.**

وَنُمَكِّنَ لَهُمۡ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَنُرِيَ فِرۡعَوۡنَ وَهَٰمَٰنَ وَجُنُودَهُمَا
مِنۡهُم مَّا كَانُواْ يَحۡذَرُونَ ٦ وَأَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰٓ أُمِّ مُوسَىٰٓ
أَنۡ أَرۡضِعِيهِۖ فَإِذَا خِفۡتِ عَلَيۡهِ فَأَلۡقِيهِ فِي ٱلۡيَمِّ وَلَا تَخَافِي
وَلَا تَحۡزَنِيٓۖ إِنَّا رَآدُّوهُ إِلَيۡكِ وَجَاعِلُوهُ مِنَ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ٧
فَٱلۡتَقَطَهُۥٓ ءَالُ فِرۡعَوۡنَ لِيَكُونَ لَهُمۡ عَدُوّٗا وَحَزَنًاۗ إِنَّ
فِرۡعَوۡنَ وَهَٰمَٰنَ وَجُنُودَهُمَا كَانُواْ خَٰطِـِٔينَ ٨
وَقَالَتِ ٱمۡرَأَتُ فِرۡعَوۡنَ قُرَّتُ عَيۡنٖ لِّي وَلَكَۖ لَا تَقۡتُلُوهُ
عَسَىٰٓ أَن يَنفَعَنَآ أَوۡ نَتَّخِذَهُۥ وَلَدٗا وَهُمۡ لَا يَشۡعُرُونَ ٩
وَأَصۡبَحَ فُؤَادُ أُمِّ مُوسَىٰ فَٰرِغًاۖ إِن كَادَتۡ لَتُبۡدِي بِهِۦ لَوۡلَآ
أَن رَّبَطۡنَا عَلَىٰ قَلۡبِهَا لِتَكُونَ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١٠ وَقَالَتۡ
لِأُخۡتِهِۦ قُصِّيهِۖ فَبَصُرَتۡ بِهِۦ عَن جُنُبٖ وَهُمۡ لَا يَشۡعُرُونَ
نصف الحزب ٣٩ ١١ ۞وَحَرَّمۡنَا عَلَيۡهِ ٱلۡمَرَاضِعَ مِن قَبۡلُ فَقَالَتۡ هَلۡ أَدُلُّكُمۡ
عَلَىٰٓ أَهۡلِ بَيۡتٖ يَكۡفُلُونَهُۥ لَكُمۡ وَهُمۡ لَهُۥ نَٰصِحُونَ
١٢ فَرَدَدۡنَٰهُ إِلَىٰٓ أُمِّهِۦ كَيۡ تَقَرَّ عَيۡنُهَا وَلَا تَحۡزَنَ وَلِتَعۡلَمَ
أَنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٞ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَهُمۡ لَا يَعۡلَمُونَ ١٣



**(6) Kuma muna son mu tabbatar da su a bayan qasa, ta hanyar sanya su masu mulki a cikinta, kuma mu nuna wa Fir'auna da babban mataimakinsa cikin mulki Hamana, da rundunoninsu masu taimaka musu a cikin mulki, abin da suka kasance suna tsoronsa na tafiyar mulkinsu, da qarewarsa a hannun wani xa namiji da za a haifa daga cikin Bani Isra'ila.**

**Yayin da Allah ya ambaci yadda mulkin Fir'auna zai qare, da abin da zai girmama Annabi Musa da mutanensa da shi, sai ya ambaci tasowar Annabi Musa har zuwa lokacin da Allah ya aike shi a matsayin Manzo, ya ce:**

**(7) Mun yi wa mahaifiyar Annabi Musa (A.S) ilhamar cewa: "Ki shayar da shi, har idan kin ji tsoron Fir'auna da mutanensa zasu kashe shi, to ki saka shi a akwati, ki jefa shi a tekun Nilu. Kada ki ji masa tsoron nutsewa, ko haxuwa da Fir'auna, kuma kar ki yi baqin cikin rabuwa da shi, tabbas zamu dawo miki da shi da ransa, kuma zamu saka shi cikin Manzannin da muke aiko su zuwa ga mutane.**

**(8) Sai ta bi abin da muka yi mata ilhamarsa, na saka shi cikin akwati, da jefa shi cikin teku. Sai iyalan Fir'ana suka tsince shi, suka xauke shi, domin abin da Allah ya yi nufi na cewa Annabi Musa zai zama abokin gabar Fir'auna, wanda Allah zai gusar da mulkinsa a hannunsa, ya jawo musu baqin ciki. Lallai Fir'auna da wazirinsa Hamana da mataimakansa sun kasance masu savo, saboda kafircinsu da shisshiginsu da varnansu a bayan qasa.**

**(9) Yayin da Fir'auna ya yi niyyar kashe shi, sai matarsa ta ce masa: "Wannan yaron shi ne sanadin farin cikina da kai. Kar ku kashe shi, tana iya yiwuwa ya amfane mu wajen hidima, ko kuma mu xauke shi a matsayin xan riqo, alhali basu san yadda mukinsu zai kasance ta hannunsa ba.**

**(10) Sai zuciyar mahaifiyar Annabi Musa ta wayi gari babu komai a cikinta na lamuran duniya face lamarin Annabi Musa, ta kasa haquri, har ma ta kusa ta bayyana cewa xanta ne, saboda tsananin shaquwarta da shi, ba don mun xaure mata zuciyarta ba, mun kafe ta, sannan mun saka mata haquri don ta zamo cikin Muminai masu dogaro ga Ubangijinsu, masu haquri a kan abin da ya qaddara.**

**(11) Sai mahaifiyar Annabi Musa tace wa 'yar uwar shi, bayan ta jefa shi cikin tekun: "Ki bi bayansa, don ki ga yadda za a yi da shi, sai ta saka masa ido daga nesa, don kar a gane lamarinta, kuma kar Fir'auna da mutanensa su gane cewa ita 'yar uwarsa ce, kuma labarinsa take bibiya.**

**(12) Sai Annabi Musa ya qi shan nonon mata masu shayarwa, a kan wani tsari na Allah. Yayin da 'yar uwarsa ta ga yadda suke qoqarin shayar da shi, sai ta ce musu: "Shin in nuna muku wasu mutanen gidan da zasu shayar da shi, su raine shi, kuma zasu kasance masu kyautata masa nasiha?".**

**(13) Sai muka mayar da Annabi Musa wurin mahaifiyarsa, don idonta ya yi sanyi, da ganinsa kusa da ita, kuma don kar ta yi baqin cikin rabuwa da shi, kuma don ta san cewa alqawarin da Allah ya yi na dawo mata da shi gaskiya ne, babu shakka a cikinsa, sai dai da yawansu basu san da wannan alqawarin ba. Kuma babu wanda ya san cewa ita ce mahaifiyarsa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Tsarin Allah da yake yi wa bayinsa nagartattu, da kuvutar da su daga makircin abokan gabarsu.**

**2 - Abin da azzalumi yake shiryawa yana iya zama sababin halakar sa. 3 - Tsananin tausayin iyaye mata ga 'ya'yansu. 4 - Halaccin yin amfani da dabara wadda shari'a ta yadda da ita, don kuvutar da kai daga zaluncin azzalumi. 5 - Tabbatuwar alqawarin Allah abu ne da babu makawar faruwarsa.**

وَلَمَّا بَلَغَ أَشُدَّهُۥ وَٱسۡتَوَىٰٓ ءَاتَيۡنَٰهُ حُكۡمٗا وَعِلۡمٗاۚ وَكَذَٰلِكَ نَجۡزِي
ٱلۡمُحۡسِنِينَ ١٤ وَدَخَلَ ٱلۡمَدِينَةَ عَلَىٰ حِينِ غَفۡلَةٖ مِّنۡ أَهۡلِهَا
فَوَجَدَ فِيهَا رَجُلَيۡنِ يَقۡتَتِلَانِ هَٰذَا مِن شِيعَتِهِۦ وَهَٰذَا مِنۡ عَدُوِّهِۦۖ
فَٱسۡتَغَٰثَهُ ٱلَّذِي مِن شِيعَتِهِۦ عَلَى ٱلَّذِي مِنۡ عَدُوِّهِۦ فَوَكَزَهُۥ
مُوسَىٰ فَقَضَىٰ عَلَيۡهِۖ قَالَ هَٰذَا مِنۡ عَمَلِ ٱلشَّيۡطَٰنِۖ إِنَّهُۥ عَدُوّٞ مُّضِلّٞ
مُّبِينٞ ١٥ قَالَ رَبِّ إِنِّي ظَلَمۡتُ نَفۡسِي فَٱغۡفِرۡ لِي فَغَفَرَ لَهُۥٓۚ إِنَّهُۥ
هُوَ ٱلۡغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ١٦ قَالَ رَبِّ بِمَآ أَنۡعَمۡتَ عَلَيَّ فَلَنۡ أَكُونَ
ظَهِيرٗا لِّلۡمُجۡرِمِينَ ١٧ فَأَصۡبَحَ فِي ٱلۡمَدِينَةِ خَآئِفٗا يَتَرَقَّبُ فَإِذَا
ٱلَّذِي ٱسۡتَنصَرَهُۥ بِٱلۡأَمۡسِ يَسۡتَصۡرِخُهُۥۚ قَالَ لَهُۥ مُوسَىٰٓ إِنَّكَ لَغَوِيّٞ
مُّبِينٞ ١٨ فَلَمَّآ أَنۡ أَرَادَ أَن يَبۡطِشَ بِٱلَّذِي هُوَ عَدُوّٞ لَّهُمَا قَالَ
يَٰمُوسَىٰٓ أَتُرِيدُ أَن تَقۡتُلَنِي كَمَا قَتَلۡتَ نَفۡسَۢا بِٱلۡأَمۡسِۖ إِن تُرِيدُ
إِلَّآ أَن تَكُونَ جَبَّارٗا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَمَا تُرِيدُ أَن تَكُونَ مِنَ ٱلۡمُصۡلِحِينَ
١٩ وَجَآءَ رَجُلٞ مِّنۡ أَقۡصَا ٱلۡمَدِينَةِ يَسۡعَىٰ قَالَ يَٰمُوسَىٰٓ إِنَّ ٱلۡمَلَأَ
يَأۡتَمِرُونَ بِكَ لِيَقۡتُلُوكَ فَٱخۡرُجۡ إِنِّي لَكَ مِنَ ٱلنَّٰصِحِينَ ٢٠
فَخَرَجَ مِنۡهَا خَآئِفٗا يَتَرَقَّبُۖ قَالَ رَبِّ نَجِّنِي مِنَ ٱلۡقَوۡمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ٢١



**Yayin da Allah ya ambacin farkon lamarin Annabi Musa (A.S) sai kuma ya ambaci samartakar sa, ya ce:**

**(14) Yayin da ya kai shekarun qarfin ciki, ya tabbatu cikin qarfinsa, sai muka bashi fahimta da ilimi cikin addinin Bani Isra'ila, kafin Annabcinsa. Kamar yadda muka saka wa Annabi Musa (A.S) a kan biyayyarsa, haka muke sakawa masu kyautatawa a kowane zamani da lokaci.**

**(15) Annabi Musa ya shiga gari a lokacin da mutane suke hutawa a cikin gidajensu, sai ya ga wasu mutne guda biyu a garin suna faxa, suna dukan juna, xayansu daga cikin Bani Isra'ila, mutanen Annabi Musa (A.S), xayan kuma daga cikin qibxawa, mutanen Fir'auna, abokin gabar Annabi Musa, sai wanda yake daga cikin mutanensa ya nemi shi da ya agaza masa a kan wanda yake daga cikin Qivxawa abokanan gabarsa, sai Annabi musa ya naushe baqibxen nan da hannunsa, sai ya kashe shi da wannan naushin, saboda qarfin dukan. Sai Annabi Musa ya ce: "Lallai wannan yana daga cikin qawatawar Shaixan da ruxinsa. Haqiqa Shaixan maqiyi ne, mai vatar da duk wanda ya bi shi, mai qiyayya a fili, don haka wannan abin da ya faru da ni, ya faru ne saboda qiyayyarsa, kuma saboda shi mai vatarwa ne yana son ya vatar da ni".**

**(16) Annabi Musa ya ce, yana mai roqon Ubangijinsa, cikin iqrarin abin da ya aikata, ya ce: "Ya Ubangijina, lallai na zalunci kaina da na kashe wannan baqibxe, ka gafarta mini zunubina". sai Allah ya bayyana mana cewa ya gafarta wa Annabi Musa. Lallai shi mai yawan gafara ne ga duk wanda ya tuba daga cikin bayinsa, mai jin qai ne a gare su.**

**(17) Sannan Allah ya ci gaba da bayar da labarin addu'ar Annabi Musa, wadda yake cewa: "Ya Ubangijina, saboda ni'imar da ka yi min ta qarfi da hikima da ilimi, to ba zan zama mai taimakon masu laifi a kan laifin su ba".**

**(18) Yayin da abin da ya faru da shi na kisan baqibxe ya faru, sai ya wayi gari a cikin garin yana cike da tsoro, da jiran mai zai faru, sai ga wanda ya nemi taimakonsa da agajinsa a kan abokin gabarsa baqibxe a jiya, yana sake neman taimakonsa a kan wani baqibxen kuma. Sai Annabi Musa ya ce masa: "Lallai kai vatacce ne bayyananne".**

**(19) Yayin da Annabi Musa ya yi nufin ya damqi baqibxen nan, wanda yake maqiyinsu ne, shi da wancan xan qabilar Bani Isra'ilar, sai wannan Bani isra'ilar ya yi zaton shi zai damqa, saboda ya ji ya ce masa (Lallai kai vatacce ne bayyananne), don haka sai ya ce wa Annabi Musa: "Shin kana son ka kashe ni ne, kamar yadda ka kashe rai jiya, ba kada wata manufa sai dai ka zama mai girman kai a bayan qasa, kana kashe mutane, kana zaluntarsu, baka nufin ka zama cikin masu yin sulhu tsakanin masu faxa da juna?!"**

**(20) Yayin da labarin ya yaxu, sai wani mutum ya zo daga can qarshen gari da sauri, don tausaya wa Annabi Musa a kan yadda ake nemansa, ya ce: "Ya kai Musa, haqiqa manyan mutanen Fir'auna suna shawarar su kashe ka, don haka ka fita daga garin nan. Lallai ina cikin masu baka shawara ta gaskiya, don ina tausaya maka, kar su kama, su kashe ka".**

**(21) Sai Annabi Musa ya bi umarnin mutumin nan mai nasiha, ya fita daga garin yana cikin tsoro, yana dakon me zai faru da shi? Sai ya ce, yana mai roqon Ubangijinsa: "Ya Ubangijina ka kuvutar da ni daga mutane azzalumai, kar su iso gare ni da wata cutarwa".**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Yin iqrari da zunubi yana daga cikin ladubban addu'a. 2 - Kyakkyawar godiya ita ce irin wanda take kai bawa zuwa ga biyayya ga Ubangijinsa, da nesantar savonsa. 3 - Muhimmancin gaggauta nasiha, musamman idan hakan zai kawo tserar da Mumini daga halaka. 4 - Wajabcin riqo da sabubban tsira, da komawa zuwa ga Allah ta hanyar addu'a.**

وَلَمَّا تَوَجَّهَ تِلْقَآءَ مَدْيَنَ قَالَ عَسَىٰ رَبِّيٓ أَن يَهْدِيَنِي سَوَآءَ
ٱلسَّبِيلِ ٢٢ وَلَمَّا وَرَدَ مَآءَ مَدْيَنَ وَجَدَ عَلَيْهِ أُمَّةٗ مِّنَ
ٱلنَّاسِ يَسْقُونَ وَوَجَدَ مِن دُونِهِمُ ٱمْرَأَتَيْنِ تَذُودَانِۖ قَالَ
مَا خَطْبُكُمَاۖ قَالَتَا لَا نَسْقِي حَتَّىٰ يُصْدِرَ ٱلرِّعَآءُۖ وَأَبُونَا
شَيْخٞ كَبِيرٞ ٢٣ فَسَقَىٰ لَهُمَا ثُمَّ تَوَلَّىٰٓ إِلَى ٱلظِّلِّ فَقَالَ
رَبِّ إِنِّي لِمَآ أَنزَلْتَ إِلَيَّ مِنْ خَيْرٖ فَقِيرٞ ٢٤ فَجَآءَتْهُ إِحْدَىٰهُمَا
تَمْشِي عَلَى ٱسْتِحْيَآءٖ قَالَتْ إِنَّ أَبِي يَدْعُوكَ لِيَجْزِيَكَ
أَجْرَ مَا سَقَيْتَ لَنَاۚ فَلَمَّا جَآءَهُۥ وَقَصَّ عَلَيْهِ ٱلْقَصَصَ قَالَ
لَا تَخَفْۖ نَجَوْتَ مِنَ ٱلْقَوْمِ ٱلظَّٰلِمِينَ ٢٥ قَالَتْ إِحْدَىٰهُمَا
يَٰٓأَبَتِ ٱسْتَـْٔجِرْهُۖ إِنَّ خَيْرَ مَنِ ٱسْتَـْٔجَرْتَ ٱلْقَوِيُّ ٱلْأَمِينُ
٢٦ قَالَ إِنِّيٓ أُرِيدُ أَنْ أُنكِحَكَ إِحْدَى ٱبْنَتَيَّ هَٰتَيْنِ عَلَىٰٓ أَن
تَأْجُرَنِي ثَمَٰنِيَ حِجَجٖۖ فَإِنْ أَتْمَمْتَ عَشْرٗا فَمِنْ عِندِكَۖ
وَمَآ أُرِيدُ أَنْ أَشُقَّ عَلَيْكَۚ سَتَجِدُنِيٓ إِن شَآءَ ٱللَّهُ مِنَ
ٱلصَّٰلِحِينَ ٢٧ قَالَ ذَٰلِكَ بَيْنِي وَبَيْنَكَۖ أَيَّمَا ٱلْأَجَلَيْنِ
قَضَيْتُ فَلَا عُدْوَٰنَ عَلَيَّۖ وَٱللَّهُ عَلَىٰ مَا نَقُولُ وَكِيلٞ ٢٨



**(22) Yayin da ya fuskanci garin Madyana, ya fara tafiya, sai ya ce: "Ina fatan Ubangijina ya shiryar da ni zuwa hanyar da ta fi alheri, kuma kada in vace daga gare ta".**

**(23) Yayin da ya isa ruwan Madyana, wanda suke shayarwa a cikinsa, sai ya ga tarin jama'a suna shayar da dabbobinsu, ya samu wasu mata guda biyu a gefe, sun tare tumakinsu daga shan ruwan, har sai mutane su gama shayarwa, sai Annabi Musa (A.S) ya ce musu: "Me yasa ba kwa shayarwa tare da mutane?" Sai suka ce masa: "Al'adarmu, muna zuwa, amma ba ma shayarwa har sai in makiyaya sun gama shayarwa sun tafi, saboda tsoron cakuxuwa da su, kuma babanmu tsoho ne, ya girma, ba zai iya shayarwa ba, wannan shi ya tilasta mana, mu shayar da tumakinmu".**

**(24) Sai ya ji tausayinsu, ya shayar musu da tumakinsu, sannan ya tafi wurin inuwa ya huta, ya roqi Ubangijinsa, yana mai bijiro da buqatarsa, ya ce: "Ya Ubangijina, lallai ni mabuqaci ne ga duk wani alherin da zaka saukar mini".**

**(25) Yayin da suka tafi, sai suka ba wa babansu labarinsa, sai ya aiko xayarsu ta kirawo shi, sai ta zo wurin shi tana tafiya cikin kunya, ta ce: "Babanmu yana kiranka, ka zo don ya baka ladan shayarwar da ka yi mana". Yayin da Annabi Musa ya je wurinsa, ya bashi labarinsa, sai ya ce masa - yana mai kwantar masa da hankali -: "Kar ka tsorata. Lallai ka tsira daga azzaluman mutane, fir'auna da 'yan qanzaginsa, domin ba su da iko a kan garin Madyana, saboda haka ba za su iya isowa gare ka da kowace irin cutarwa ba".**

**(26) Sai xaya cikin 'ya'yansa mata ta ce: "Ya Baba, ka dauke shi qwadago, ya riqa shayarwa mana da tumakinmu, don ya cancanta ka xauke shi qwadago, saboda ya haxa qarfi da amana. Da qarfinsa zai aiwatar da abin da aka xora masa, da amanarsa kuma zai kiyaye abin da aka ba shi amanarsa".**

**(27) Sai babansu ya ce, yana mai magana da Annabi Musa (A.S): "Lallai ina son in aurar maka da xaya daga cikin waxannan 'ya'yan mata nawa guda biyu, a kan cewa sadakinta shi ne zaka yi kiwon tumakinmu tsawon shekaru takwas, amma in ka cika adadin zuwa shekaru goma, to wannan kyautatawa ne daga gare ka, ba dole ba ne a kanka, saboda yarjejeniyar a kan shekaru takwas ne. Saboda haka abin da ya qaru a kan haka to nafila ne, Ba na son in xora maka abin da zai saka ka cikin wahala. Da sannu za ka same ni –in Allah ya so- cikin masu nagarta, waxanda suke cika alqawari, kuma ba sa karya alqawari".**

**(28) Sai Annabi Musa (A.S) ya ce: "Wancan abin da yake tsakanina da kai yana nan, kamar yadda muka yi yarjejjeniya a kai. Kowanne ne cikin lokutan guda biyun na yi maka, shekaru takwas ko goma, to zan zama na cika abin da ya wajaba a kaina, ba zaka neme ni da wani qari ba. Kuma Allah shi ne wakili a kan abin da muka qulla yarjejjeniya a kai, kuma mai saka ido a kai".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Komawa zuwa ga Allah hanya ce ta tsira a duniya da lahira.**
**2 - Kunyar 'ya Musulma sababi ne na girmanta da xaukakar lamarinta.**
**3 - Tarayya da mace a cikin ra'ayi, da karxan ra'ayinta in ya zama daidai, abin yabawa ne.**
**4 - Qarfi da amana sune siffofin ma'aikaci mai cin nasara.**
**5 - Halaccin a yi sadaki da wani amfani da za a samu daga miji.**

ثلاثة أرباع الحزب ٣٩

۞ فَلَمَّا قَضَىٰ مُوسَى ٱلْأَجَلَ وَسَارَ بِأَهْلِهِۦٓ ءَانَسَ مِن جَانِبِ
ٱلطُّورِ نَارًاۖ قَالَ لِأَهْلِهِ ٱمْكُثُوٓاْ إِنِّيٓ ءَانَسْتُ نَارًا لَّعَلِّيٓ ءَاتِيكُم
مِّنْهَا بِخَبَرٍ أَوْ جَذْوَةٍ مِّنَ ٱلنَّارِ لَعَلَّكُمْ تَصْطَلُونَ ٢٩
فَلَمَّآ أَتَىٰهَا نُودِيَ مِن شَٰطِيِٕ ٱلْوَادِ ٱلْأَيْمَنِ فِي ٱلْبُقْعَةِ
ٱلْمُبَٰرَكَةِ مِنَ ٱلشَّجَرَةِ أَن يَٰمُوسَىٰٓ إِنِّيٓ أَنَا ٱللَّهُ رَبُّ
ٱلْعَٰلَمِينَ ٣٠ وَأَنْ أَلْقِ عَصَاكَۚ فَلَمَّا رَءَاهَا تَهْتَزُّ كَأَنَّهَا
جَآنٌّ وَلَّىٰ مُدْبِرًا وَلَمْ يُعَقِّبْۚ يَٰمُوسَىٰٓ أَقْبِلْ وَلَا تَخَفْۖ
إِنَّكَ مِنَ ٱلْءَامِنِينَ ٣١ ٱسْلُكْ يَدَكَ فِي جَيْبِكَ تَخْرُجْ
بَيْضَآءَ مِنْ غَيْرِ سُوٓءٍ وَٱضْمُمْ إِلَيْكَ جَنَاحَكَ مِنَ ٱلرَّهْبِۖ
فَذَٰنِكَ بُرْهَٰنَانِ مِن رَّبِّكَ إِلَىٰ فِرْعَوْنَ وَمَلَإِيْهِۦٓۚ إِنَّهُمْ
كَانُواْ قَوْمًا فَٰسِقِينَ ٣٢ قَالَ رَبِّ إِنِّي قَتَلْتُ مِنْهُمْ نَفْسًا
فَأَخَافُ أَن يَقْتُلُونِ ٣٣ وَأَخِي هَٰرُونُ هُوَ أَفْصَحُ مِنِّي لِسَانًا
فَأَرْسِلْهُ مَعِيَ رِدْءًا يُصَدِّقُنِيٓۖ إِنِّيٓ أَخَافُ أَن يُكَذِّبُونِ ٣٤
قَالَ سَنَشُدُّ عَضُدَكَ بِأَخِيكَ وَنَجْعَلُ لَكُمَا سُلْطَٰنًا فَلَا
يَصِلُونَ إِلَيْكُمَا بِـَٔايَٰتِنَآۚ أَنتُمَا وَمَنِ ٱتَّبَعَكُمَا ٱلْغَٰلِبُونَ ٣٥



**(29) Yayin da Annabi Musa ya cika mafi tsawon lokacin biyu, wato shekaru goma, ya taho da iyalansa daga Madyana zuwa Misra, sai ya ga wata wuta a gefen duten Xur, sai ya ce wa iyalansa: "ku tsaya a nan, na ga wata wuta, wataqila in zo muku da wani labari daga wurinta, ko in zo muku da bakin wuta, wanda zaku kunna, ko kwa ji ximi da shi daga sanyi".**

**(30) Yayin da Annabi Musa ya je wurin wutar da ya gani, sai Ubangijinsa Maxaukakin Sarki ya kira shi daga gefen kwari na dama, a wurin da Allah ya albarkace shi da magana da Annabi Musa, wajen bishiya, ya ce: "Ya kai Musa, haqiqa ni ne Ubangijin halitta gaba xayansu".**

**(31) "Ka jefar da sandarka". Sai Annabi Musa ya jefar da ita saboda biyaya ga umarnin Ubangijinsa. Yayin da ya gan ta tana motsi, tana tafiya kamar macijiya wajen saurinta, sai ya juya a guje saboda tsoronta, bai dawo ba. Sai Ubangijinsa ya kira shi da cewa: "Ya kai Musa, dawo, kada ka ji tsoronta, kai kana cikin amintattu daga gare ta, da ma duk wani abin da kake jin tsoronsa".**

**(32) Ka shigar da hanunka na dama a cikin wuyan rigarka, zai fito fari ba tare da wani ciwo ba. Sai Annabi Musa ya shigar da shi, sai ya fito fari fat kamar qanqara. Kuma ka haxa hannuwanka zuwa jikinka, don tsoronka ya tafi. Sai Annabi Musa ya haxa su, sai tsoron ya tafi. Waxannan abubuwa guda biyu da aka ambata – sanda da hannu- hujjoji ne guda biyu da aka aiko su daga Ubangijinka zuwa ga Fir'auna da manyan mutanensa, lallai su sun kasance mutane ne masu fita daga biyayyar Allah da kafirci da savo.**

**(33) Sai Annabi Musa ya yi kamun qafa zuwa ga Ubangijinsa, ya ce,: "Lallai na kashe wani mutum a cikinsu, don haka ina tsoron su kashe ni a madadinsa, in na je in isar musu da saqon da aka turo ni da shi".**

**(34) Kuma xan uwana Haruna ya fi ni iya bayyana zance, ka aiko shi tare da ni, ya zama mataimakina wanda zai mara mini baya cikin zancena, idan Fir'auna da Mutanensa sun qaryata ni. Lallai in jin tsoron zasu qaryata ni, kamar yadda yake shi ne al'adar al'ummun da aka tura musu Manzanni gabani na, sun qaryata Manzannin.**

**(35) Sai Allah ya amsa addu'ar Annabi Musa, ya ce: "Da sannu zamu qarfafa maka gwiwa – Ya kai Musa- ta hanyar aiko da xan 'uwanka tare da kai, a matsayin Manzo, kuma mataimakinka, kuma mu baku hujja da qarfafawa, ta yadda ba za su iya isa gare ku da wani abin da kuke qi ba, saboda da ayoyinmu da muka aiko ku da su. ku biyun da waxanda suka bi ku, daga cikin muminai, ku ne masu nasara.**

## Kaxan Daga Abi Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Cika yarjejjeniya aiki ne na Muminai.**
**2 - Maganar Allah da Annabi Musa (A.S) magana ce ta haqiqa.**
**3 - Buqatuwar mai kira zuwa ga Allah ga wanda zai mara masa baya.**
**4 - Muhimmancin fasahar zance ga masu da'awa.**

فَلَمَّا جَآءَهُم مُّوسَىٰ بِـَٔايَٰتِنَا بَيِّنَٰتٖ قَالُواْ مَا هَٰذَآ إِلَّا سِحۡرٞ
مُّفۡتَرٗى وَمَا سَمِعۡنَا بِهَٰذَا فِيٓ ءَابَآئِنَا ٱلۡأَوَّلِينَ ٣٦
وَقَالَ مُوسَىٰ رَبِّيٓ أَعۡلَمُ بِمَن جَآءَ بِٱلۡهُدَىٰ مِنۡ عِندِهِۦ وَمَن
تَكُونُ لَهُۥ عَٰقِبَةُ ٱلدَّارِۚ إِنَّهُۥ لَا يُفۡلِحُ ٱلظَّٰلِمُونَ ٣٧
وَقَالَ فِرۡعَوۡنُ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡمَلَأُ مَا عَلِمۡتُ لَكُم مِّنۡ إِلَٰهٍ
غَيۡرِي فَأَوۡقِدۡ لِي يَٰهَٰمَٰنُ عَلَى ٱلطِّينِ فَٱجۡعَل لِّي صَرۡحٗا لَّعَلِّيٓ
أَطَّلِعُ إِلَىٰٓ إِلَٰهِ مُوسَىٰ وَإِنِّي لَأَظُنُّهُۥ مِنَ ٱلۡكَٰذِبِينَ ٣٨
وَٱسۡتَكۡبَرَ هُوَ وَجُنُودُهُۥ فِي ٱلۡأَرۡضِ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّ وَظَنُّوٓاْ
أَنَّهُمۡ إِلَيۡنَا لَا يُرۡجَعُونَ ٣٩ فَأَخَذۡنَٰهُ وَجُنُودَهُۥ فَنَبَذۡنَٰهُمۡ
فِي ٱلۡيَمِّۖ فَٱنظُرۡ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلظَّٰلِمِينَ ٤٠
وَجَعَلۡنَٰهُمۡ أَئِمَّةٗ يَدۡعُونَ إِلَى ٱلنَّارِۖ وَيَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ
لَا يُنصَرُونَ ٤١ وَأَتۡبَعۡنَٰهُمۡ فِي هَٰذِهِ ٱلدُّنۡيَا لَعۡنَةٗۖ
وَيَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ هُم مِّنَ ٱلۡمَقۡبُوحِينَ ٤٢ وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا
مُوسَى ٱلۡكِتَٰبَ مِنۢ بَعۡدِ مَآ أَهۡلَكۡنَا ٱلۡقُرُونَ ٱلۡأُولَىٰ
بَصَآئِرَ لِلنَّاسِ وَهُدٗى وَرَحۡمَةٗ لَّعَلَّهُمۡ يَتَذَكَّرُونَ ٤٣



**(36) Yayin da Annabi Musa (A.S) ya zo musu da ayoyinmu bayyanannu, sai suka ce: “Wannan ba komai ba ne face qagaggen abu, wanda Musa ya qago shi, ba mu tava jin wannan daga wurin iyayenmu na farko ba”.**

**(37) Annabi Musa ya ce, yana mai magana da Fir'auna: “Ubangijina ya san wanene mai gaskiya, wanda ya zo da shiriya daga wajen Allah, kuma ya san wane ne qarshen lamarinsa zai yi kyau a lahira. Lallai azzalumai ba sa rabauta da abin da suke nema, kuma ba sa kuvuta daga abin da suke jin tsoronsa.**

**(38) Fir'auna ya ce, yana mai magana da manyan mutanensa: “Ya ku manyan mutanena, ban san wani abin bautar ku ba, koma bayana. Ya kai Hamana! kunna mini wuta a kan bulon tavon nan, don ya yi qarfi, sai ka yi mini gini mai tsayi (bene), ko zan ga abin bautar Musa, in tsaya a kansa. Kai! lallai ni ina zaton Musa maqaryaci ne, cikin abin da yake iqrarinsa, na cewa shi Manzo ne daga wurin Allah zuwa gare ni da mutanena”.**

**(39) Girman kan Fir'auna da sojojinsa ya qara tsanani, suka xaukaka a qasar Misra, ba tare da wani dalili na gaskiya ba, kuma suka kore yiwuwar tashi bayan mutuwa, suka yi zaton cewa ba ba za a mayar da su, zuwa gare mu ba, a ranar alqiyama don yin hisabi da uquba.**

**(40) Sai Muka damqe shi da sojojinsa, muka jefa su cikin teku, suka nitse, har sai da suka halaka gaba xayansu. Ka yi tunani – Ya kai wannan Manzo- yadda makomar lamarin azzalumai da qarshensu ta kasance. Makomarsu da qarshensu ya kasance halaka ne.**

**(41) Muka sanya su, suka zama abin koyin wajen masu qetare iyaka da vatattu, suna kira zuwa ga wuta, ta hanyar abubuwan da suke yaxawa na kafirci da vata. Kuma a ranar alqiyama ba za a agaza musu a tsamar da su daga azaba ba. Za a ruvanya musu azaba saboda abin da suka qirqira na mummunan tafarki, da abin da suka kira mutane zuwa gare shi na vata, za a rubuta musu zunubin aikinsu da suka yi na vata, da zunubin aikin wanxanda suka yi musu biyayya wajen aiki da vata.**

**(42) Muka bi bayansu da tavewa da la'anta, qari a kan uqubar gidan duniya, sannan a ranar alqiyama suna cikin abubuwan zargi, waxanda ake nisantar da su daga rahamar Allah.**

**(43) Haqiqa mun bai wa Annabi Musa (A.S) Attaura, bayan mun aika wa al'ummun da suka gabata Manzanninmu, suka qaryata su, sai muka halakar da su, saboda qaryata su da suka yi. A cikin Attaura akwai abin da zai nunawa mutane abin da zai amfane su, su yi aiki da shi, da abin da zai cutar da su, su guje shi, haka nan a cikinta akwai shiriyarsu zuwa alheri da rahama, saboda abin da ta qunsa na alherin duniya da lahira, ko sa tuna ni'imomin Allah a kansu, sai su gode masa, su yi imani da shi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Kore gaskiya da shubuhohi masu rauni aikin ma'abota shisshigi ne.**
**2 - Girman kai yana hana bin gaskiya.**
**3 - Mummunan qarshen masu girman kai, yana daga cikin sunnonin Ubangijin talikai.**
**4 - Qarya tana da jagororinta, da masu kira zuwa gare ta, da fuskokinta da kamanninta.**

وَمَا كُنتَ بِجَانِبِ ٱلْغَرْبِيِّ إِذْ قَضَيْنَآ إِلَىٰ مُوسَى ٱلْأَمْرَ وَمَا كُنتَ
مِنَ ٱلشَّٰهِدِينَ ﴿٤٤﴾ وَلَٰكِنَّآ أَنشَأْنَا قُرُونًا فَتَطَاوَلَ عَلَيْهِمُ
ٱلْعُمُرُ ۚ وَمَا كُنتَ ثَاوِيًا فِىٓ أَهْلِ مَدْيَنَ تَتْلُوا۟ عَلَيْهِمْ
ءَايَٰتِنَا وَلَٰكِنَّا كُنَّا مُرْسِلِينَ ﴿٤٥﴾ وَمَا كُنتَ بِجَانِبِ
ٱلطُّورِ إِذْ نَادَيْنَا وَلَٰكِن رَّحْمَةً مِّن رَّبِّكَ لِتُنذِرَ قَوْمًا
مَّآ أَتَىٰهُم مِّن نَّذِيرٍ مِّن قَبْلِكَ لَعَلَّهُمْ يَتَذَكَّرُونَ ﴿٤٦﴾
وَلَوْلَآ أَن تُصِيبَهُم مُّصِيبَةٌۢ بِمَا قَدَّمَتْ أَيْدِيهِمْ فَيَقُولُوا۟
رَبَّنَا لَوْلَآ أَرْسَلْتَ إِلَيْنَا رَسُولًا فَنَتَّبِعَ ءَايَٰتِكَ وَنَكُونَ
مِنَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ﴿٤٧﴾ فَلَمَّا جَآءَهُمُ ٱلْحَقُّ مِنْ عِندِنَا قَالُوا۟
لَوْلَآ أُوتِىَ مِثْلَ مَآ أُوتِىَ مُوسَىٰٓ ۚ أَوَلَمْ يَكْفُرُوا۟ بِمَآ أُوتِىَ
مُوسَىٰ مِن قَبْلُ ۖ قَالُوا۟ سِحْرَانِ تَظَٰهَرَا وَقَالُوٓا۟ إِنَّا بِكُلٍّ كَٰفِرُونَ
﴿٤٨﴾ قُلْ فَأْتُوا۟ بِكِتَٰبٍ مِّنْ عِندِ ٱللَّهِ هُوَ أَهْدَىٰ مِنْهُمَآ أَتَّبِعْهُ
إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ﴿٤٩﴾ فَإِن لَّمْ يَسْتَجِيبُوا۟ لَكَ فَٱعْلَمْ
أَنَّمَا يَتَّبِعُونَ أَهْوَآءَهُمْ ۚ وَمَنْ أَضَلُّ مِمَّنِ ٱتَّبَعَ هَوَىٰهُ بِغَيْرِ
هُدًى مِّنَ ٱللَّهِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٥٠﴾



**(44) Ya kai wannan manzo - baka nan a gefen dutse, ta vangaren yamma da inda Annabi Musa (A.S) yake tsaye, yayin da muka yanke lamarin aika shi zuwa ga Fir'auna da mutanensa, baka nan ballantana ka san wannan labarin, har ka bayar da shi ga mutane. Dan haka duk abin da kake basu labarinsa yana daga cikin wahayin da Allah ya yi maka ne.**

**(45) Sai dai mu, mun tayar da wasu al'ummu da halittu bayan Annabi Musa, sai zamani ya yi tsawo har suka manta da alqawuran Allah. Kuma baka kasance mazaunin gari a cikin mutanen Madyana, kana karanta musu ayoyinmu ba, sai dai mun aiko ka daga wurinmu, muka yi maka wahayin labarin Annabi Musa da zamansa a garin Madyana, ka ba mutane labarin abin da muka yi maka wahayinsa daga cikin hakan.**

**(46) Kuma baka kasance a gefen dutse ba, a lokacin da muka kira Annabi Musa, muka yi masa wahayin abin da muka yi masa wahayi da shi, ballantana ka bayar da labarinsa ga mutane. Sai dai mu, mun aiko ka rahama daga Ubangijinka zuwa ga mutane, sai muka yi maka wahayin labarin hakan, don ka gargaxi mutanen da wani Manzo mai gargaxi bai zo musu ba gabaninka, ko sa ji wa'azi, su yi imani da abin da ka zo musu da shi daga wurin Allah, tsarki ya tabbata a gare shi.**

**(47) Ba don kada wata uquba daga Allah ta shafe su ba, saboda abin da suke kai na kafirci da savo, su ce - suna masu kafa hujja da rashin aiko musu da Manzo -: "Ai da ka aiko mana da Manzo, da mun bi ayoyinka, mun yi aiki da su, mu zama daga cikin Muminai, masu aikata umarnin Ubangijinsu", ba domin haka ba, da mun gaggauta yi musu azaba. Amma dai mun jinkirta ta a gare su, saboda mu yanke musu hanzari da turo musu da Manzo.**

**(48) Yayin da Annabi Muhammad (S.A.W) ya zo wa Quraishawa da saqo daga wurin Ubangijinsa, sai suka tambayi Yahudawa dangane da shi, sai suka laqqana musu wannan hujjar, suka ce: "Ina ma dai an ba wa Muhammadu irin abin da aka ba wa Musa na ayoyi masu nuni cewa shi Manzo ne daga Ubangijinsa, kamar su hannu da sanda". To ka ce da su – Ya kai wannan Manzo- kana mai mayar musu da martani, cewa: "Ashe Yahudawa ba su kafirce wa abin da aka ba wa Musa tun da farko ba, suka ce - dangane da Attaura da Alqur'ani -: "Haqiqa su sihiri ne guda biyu, waxanda suke qarfafar juna". suka ci gaba da cewa, "Mun kafirce wa kowanne daga cikinsu, Attaurar da Alqur'ani?!".**

**(49) Ka ce wa waxannan – Ya kai wannan Manzo -: "Ku zo da wani littafi saukakke daga wurin Allah, wanda ya fi Attaura da Alqur'ani shiryarwa zuwa ga tafarkin madaidaici. In har kun zo da shi, to zan bi shi, in kun kasance masu gaskiya cikin iqrarinku na cewa Attaura da Alqur'ani sihiri ne".**

**(50) Idan har Quraishawa ba su amsa maka abin da ka nema a wurinsu ba, na kawo wani saukakken littafi daga wurin Allah, wanda shiriyarsa tafi ta Attaura da Alqur'ani, to ka tabbata qaryatawar su ga Attaura da Alqur'ani ba kan wani dalili ba ne, kaxai bin son zuciya ne. Kuma babu wanda ya fi nesa cikin vata sama da wanda ya bi son zuciyarsa, ba tare da wata shiriya daga Allah ba. Lallai Allah baya yin dace zuwa ga shiriya ga mutanen da suke zaluntar kawunansu da kafircewarsu ga Allah.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Kore sanin gaibu daga Manzon Allah (S.A.W) face abin da Allah ya sanar da shi.**
**2 - Qarewar ilimin da shuxewar zamani.**
**3 - Yin qalubale ga kafirai da su kawo wani abin da ya fi wahayin da Allah ya yi wa Manzanninsa shiryarwa.**
**4 - Vatan kafirai saboda bin son zuciya ne, ba a saboda bin dalili ba ne.**

الحزب ٤٠

* وَلَقَدْ وَصَّلْنَا لَهُمُ الْقَوْلَ لَعَلَّهُمْ يَتَذَكَّرُونَ ٥١ الَّذِينَ
آتَيْنَاهُمُ الْكِتَابَ مِن قَبْلِهِ هُم بِهِ يُؤْمِنُونَ ٥٢ وَإِذَا يُتْلَىٰ
عَلَيْهِمْ قَالُوا آمَنَّا بِهِ إِنَّهُ الْحَقُّ مِن رَّبِّنَا إِنَّا كُنَّا مِن قَبْلِهِ
مُسْلِمِينَ ٥٣ أُولَٰئِكَ يُؤْتَوْنَ أَجْرَهُم مَّرَّتَيْنِ بِمَا صَبَرُوا وَيَدْرَءُونَ
بِالْحَسَنَةِ السَّيِّئَةَ وَمِمَّا رَزَقْنَاهُمْ يُنفِقُونَ ٥٤ وَإِذَا سَمِعُوا
اللَّغْوَ أَعْرَضُوا عَنْهُ وَقَالُوا لَنَا أَعْمَالُنَا وَلَكُمْ أَعْمَالُكُمْ سَلَامٌ
عَلَيْكُمْ لَا نَبْتَغِي الْجَاهِلِينَ ٥٥ إِنَّكَ لَا تَهْدِي مَنْ أَحْبَبْتَ
وَلَٰكِنَّ اللَّهَ يَهْدِي مَن يَشَاءُ ۚ وَهُوَ أَعْلَمُ بِالْمُهْتَدِينَ ٥٦
وَقَالُوا إِن نَّتَّبِعِ الْهُدَىٰ مَعَكَ نُتَخَطَّفْ مِنْ أَرْضِنَا ۚ أَوَلَمْ
نُمَكِّن لَّهُمْ حَرَمًا آمِنًا يُجْبَىٰ إِلَيْهِ ثَمَرَاتُ كُلِّ شَيْءٍ رِّزْقًا
مِّن لَّدُنَّا وَلَٰكِنَّ أَكْثَرَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ٥٧ وَكَمْ أَهْلَكْنَا مِن
قَرْيَةٍ بَطِرَتْ مَعِيشَتَهَا ۖ فَتِلْكَ مَسَاكِنُهُمْ لَمْ تُسْكَن مِّن
بَعْدِهِمْ إِلَّا قَلِيلًا ۖ وَكُنَّا نَحْنُ الْوَارِثِينَ ٥٨ وَمَا كَانَ رَبُّكَ
مُهْلِكَ الْقُرَىٰ حَتَّىٰ يَبْعَثَ فِي أُمِّهَا رَسُولًا يَتْلُو عَلَيْهِمْ
آيَاتِنَا ۚ وَمَا كُنَّا مُهْلِكِي الْقُرَىٰ إِلَّا وَأَهْلُهَا ظَالِمُونَ ٥٩



**(51) Haqiqa mun isar wa Mushirikai da Yahudawan Bani Isr'aila labarin al'ummun da suka gabata, da abin da muka saukar da shi a kansu na azaba, yayin da suka qaryata Manzannimu, da fatan ko sa wa'azantu da hakan, su yi imani, don kada abin da ya sami waxancan, ya same su.**

**(52) Waxanda suka tabbata a kan imani da Attaura tun kafin a saukar da Alqur'ani, su ne waxanda suke yin imani da Alqur'ani, saboda abin da suka samu a littafansu na labarinsa da siffofinsa.**

**(53) Kuma idan ana karanta shi a gare su sai su ce: “Mun yi imani da shi. Shi ne gaskiyar da babu shakka a cikinta. Sauqaqqe daga Ubangijinmu, kuma mun kasance tun kafin saukar da wannan Alqur'anin Musulmai ne, saboda imaninmu da abin da Manzanni suka zo da shi gabaninsa”.**

**(54) Waxannan da suka siffantu da abin da aka ambata, Allah zai basu ladan ayyukansu sau biyu, saboda haqurinsu wajen imani da littafinsu, da imaninsu da Annabi Muhammad (S.A.W) yayin da aka aiko shi, kuma suna tunkuxe zunubansu da kyawawan ayyukansu, sannan daga abin da muka azurta su, suke ciyarwa a cikin ayyukan alheri. (55) Idan waxannan Muminai daga cikin Ahlul-kitabi suka ji yasasshen zance, sai su kawar da kai, ba zasu damu da shi ba, su ce, suna masu magana da masu wannan zancen, su ce: “Sakamakon ayyukanmu namu ne, ku ma sakamakon ayyukanku naku ne, kun kuvuta daga zagi da cutarwa daga gare mu, ba ma qaunar zama da jahilai, saboda abin da yake cikinsa na cutarwa a addinin da duniya.**

**(56) Haqiqa kai -Ya kai wannan Manzo- ba ka shiryar da wanda kake so, kamar Abu Xalib da waninsa, ta yadda zaka datar da shi zuwa ga imani. Allah shi kaxai yake datar da wanda ya ga dama zuwa ga shiriya. Kuma shi ne mafi sanin wanda ya gabata a cikin iliminsa cewa yana cikin shiryayyu zuwa tafarki madaidaici.**

**(57) Mushirikai daga cikin mutanen Makka suka ce, suna masu bayar da uzurin rashin bin Musulunci da imani da shi: “In har muka bi wannan Musuluncin da ka zo da shi, to abokanan gabarmu za su qwace mana qasarmu daga wurin mu da sauri”. Yanzu ashe bamu tabbatar da waxannan Mushirikai a cikin harami mai aminci ba, wanda zubar da jini da zalunci ya haramta a cikinsa, suna cikin aminci a cikinsa, daga wani ya kawo musu hari, ana kawo 'ya'yan itacen kowace irin bishiya cikinsa, arziqi daga gare mu, wanda muka koro shi zuwa gare su ba?!. Sai dai mafi yawansu basu san abin da Allah ya yi musu ni'ima da shi ba, ballantana su gode masa a kai.**

**(58) Alqaryun da suka butulce wa ni'imar Allah a kansu suna da yawa, suka wuce gona da iri cikin zunubi da savo, sai muka aiko musu da azaba, muka halaka su da ita. Waxannan wuraren zamansu ne sun rushe, mutane suna bi ta wurin, babu wanda ya sake zama a cikinsu bayansu, sai 'yan kaxan cikin masu wucewa. Kuma mun kasance mu ne masu gado, waxanda muke gadon sammai da qassai da abin da ke cikinsu.**

**(59) Ya kai wannan Manzo- Ubangijinka bai kasance mai halaka alqaryu ba, face sai bayan ya yanke wa mutanensu uzuri, ta hanyar aiko da Manzo zuwa a babban garin, kamar yadda ya aiko ka a cikin uwar Alqaryu, wato Makkah. Kuma bamu kasance waxanda zamu halaka mutanen alqaryu ba, alhali suna tsaye a kan gaskiya. Kaxai muna halakar da su ne, in sun kasance azzalumai, ta hanyar kafirci da aikata savo.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Fifikon wanda yayi imani da Annabi Muhammad (S.A.W) cikin Ahlul-kitabi da bayanin cewa yana da lada sau biyu. 2 - Shiriyar dacewa tana hannun Allah, ba ta hannun waninsa daga cikin Manzanni ko waninsu. 3 - Bin gaskiya hanya ce ta samun aminci, ba abin da yake kawo tsoro ba ne, kamar yadda Mushirikai suke da'awa.**
**4 - Haxarin jin daxin da ya wuce kima, a kan xaixaikun mutane da jama'a.**
**5 - Yana daga cikin rahamar Allah, ba ya halaka mutane, sai bayan ya yanke musu uzuri da aiko Manzanni.**

وَمَآ أُوتِيتُم مِّن شَيۡءٖ فَمَتَٰعُ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَزِينَتُهَاۚ وَمَا عِندَ
ٱللَّهِ خَيۡرٞ وَأَبۡقَىٰٓۚ أَفَلَا تَعۡقِلُونَ ٦٠ أَفَمَن وَعَدۡنَٰهُ وَعۡدًا حَسَنٗا
فَهُوَ لَٰقِيهِ كَمَن مَّتَّعۡنَٰهُ مَتَٰعَ ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا ثُمَّ هُوَ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ
مِنَ ٱلۡمُحۡضَرِينَ ٦١ وَيَوۡمَ يُنَادِيهِمۡ فَيَقُولُ أَيۡنَ شُرَكَآءِيَ
ٱلَّذِينَ كُنتُمۡ تَزۡعُمُونَ ٦٢ قَالَ ٱلَّذِينَ حَقَّ عَلَيۡهِمُ ٱلۡقَوۡلُ رَبَّنَا
هَٰٓؤُلَآءِ ٱلَّذِينَ أَغۡوَيۡنَآ أَغۡوَيۡنَٰهُمۡ كَمَا غَوَيۡنَاۖ تَبَرَّأۡنَآ إِلَيۡكَۖ
مَا كَانُوٓاْ إِيَّانَا يَعۡبُدُونَ ٦٣ وَقِيلَ ٱدۡعُواْ شُرَكَآءَكُمۡ فَدَعَوۡهُمۡ
فَلَمۡ يَسۡتَجِيبُواْ لَهُمۡ وَرَأَوُاْ ٱلۡعَذَابَۚ لَوۡ أَنَّهُمۡ كَانُواْ يَهۡتَدُونَ
٦٤ وَيَوۡمَ يُنَادِيهِمۡ فَيَقُولُ مَاذَآ أَجَبۡتُمُ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ٦٥
فَعَمِيَتۡ عَلَيۡهِمُ ٱلۡأَنۢبَآءُ يَوۡمَئِذٖ فَهُمۡ لَا يَتَسَآءَلُونَ ٦٦ فَأَمَّا
مَن تَابَ وَءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحٗا فَعَسَىٰٓ أَن يَكُونَ مِنَ ٱلۡمُفۡلِحِينَ
٦٧ وَرَبُّكَ يَخۡلُقُ مَا يَشَآءُ وَيَخۡتَارُۗ مَا كَانَ لَهُمُ ٱلۡخِيَرَةُۚ سُبۡحَٰنَ
ٱللَّهِ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ٦٨ وَرَبُّكَ يَعۡلَمُ مَا تُكِنُّ
صُدُورُهُمۡ وَمَا يُعۡلِنُونَ ٦٩ وَهُوَ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ لَهُ
ٱلۡحَمۡدُ فِي ٱلۡأُولَىٰ وَٱلۡأٓخِرَةِۖ وَلَهُ ٱلۡحُكۡمُ وَإِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ٧٠



**Yayin da Mushirikai suka bayar da uzurin qin bin gaskiya da abubuwan da suke gamuwa da su na wahalhalun yaqi, da yankewar kasuwanci, sai Allah ya basu amsa da cewa:**

**60 Duk abin da Ubangijinku ya ba ku, to yana daga cikin abin da kuke jin daxi da ado da shi a duniya, sannan sai ya qare. Amma abin da yake wurin Allah na lada mai girma a lahira, shi ne mafi alheri da wanzuwa, sama da abin da ya ke cikin duniya na jin daxi da qawa. Shin ba kwa hankaltar haka ne, ku fifita mai wanzuwa a kan mai qarewa?!.**

**61 Shin wanda muka yi masa alqawarin Aljannah a lahira, da abin da yake cikinta na ni'imomi masu wanzuwa, daidai yake da wanda muka bashi abin da yake jin daxi da shi, na dukiya da qawa a rayuwar duniya, sannan ya kasance a ranar alqiyama cikin waxanda za a halartar da su zuwa wutar Jahannama?!.**

**62 Ranar da Ubangijinsu (S.W.T) zai kira su, ya ce: "Ina abokan tarayyata da kuka kasance kuna bauta musu koma bayana, kuna riya cewa su abokanan tarayyata ne?!"**

**63 Sai waxanda azaba ta faxa a kansu, cikin masu kira zuwa ga kafirci su ce: "Ya Ubangijinmu, waxannan su ne waxanda muka vatar da su, kamar yadda muka vata, mu yi barranta daga gare su, zuwa gare ka, ba mu suke bautawa ba. Kaxai sun kasance suna bautawa Shaixanu ne kawai".**

**64 Za a ce musu: "ku kira abokanan tarayyarku, domin su tserar da ku daga abin da kuke ciki na qasqanci, sai su kira abokan tarayyar nasu, amma ba zasu amsa musu kiransu ba, kuma zasu ga azabar da aka tanadar musu, a lokacin sai su yi burin ina ma da sun kasance shiryayyu ne su a duniya.**

**65 Ranar da Ubangijinsu zai kira su, ya ce: "Me kuka amsawa Manzanni na waxanda na aiko su zuwa gare ku?".**

**66 Sai hujjar da za su faxa ba vace musu, ba za su ambaci komai ba. Kuma sashensu ba zai tambayi sashe ba, saboda abin da suke ciki na tsananin firgita, saboda yaqinin da suke da shi na azabar da take makomarsu.**

**67 Amma wanda ya tuba cikin waxannan Mushirikai daga kafircinsa, ya yi imani da Allah da Manzanninsa, kuma ya yi aiki nagari, to wannan ya kusata ya kasance cikin masu rabauta da abin da suke nema, da kuvuta daga abin da suke jin tsoronsa.**

**68 Ubangijinka - Ya kai wannan Manzo- yana halittar duk abin da ya ga dama ya halicce shi, kuma yana zavan wanda ya so ya zave shi, don biyayya gare shi da ba shi Annabcin sa. Mushirikai basu damar zavi, ballantana su ce don me Allah ya yi kaza. Allah ya tsarkaka daga abin da suke yi bautawa tare da shi, daga abokan tarayya.**

**69 Ubangijinka ya san abubuwan da zukatansu suka voye, da abubuwan da suka bayyana, babu wani abu a ciki da yake vuya a gare shi, kuma da sannu zai saka musu a kan haka.**

**70 Shi ne Allah (S.W.T) wanda babu abin bauta da gaskiya koma bayansa, shi kaxai ne abin godiya a duniya, kuma shi ne abin godiya a lahira, shi ne wanda yake da hukunci abin zartarwa, wanda babu mai mayar da shi, kuma zuwa gare shi, shi kaxai za a mayar da ku a ranar alqiyama don yin hisabi da bada sakamako.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Mai hankali shi ne wanda yake fifita mai wanzuwa a kan mai qarewa.**
**2 - Tuba tana kankare abin da ya gabace ta.**
**3 - Zavi na Allah ne, ba na bayinsa ba ne, don haka bai dace su sava masa, ko su yi karo da shi a cikin zavinsa ba.**
**4 - Kewayewar ilimin Allah da abin da ya bayyana, da abin da ya vuya, cikin ayyukan bayinsa.**

قُلْ أَرَءَيْتُمْ إِن جَعَلَ ٱللَّهُ عَلَيْكُمُ ٱلَّيْلَ سَرْمَدًا إِلَىٰ يَوْمِ
ٱلْقِيَٰمَةِ مَنْ إِلَٰهٌ غَيْرُ ٱللَّهِ يَأْتِيكُم بِضِيَآءٍ ۖ أَفَلَا تَسْمَعُونَ
٧١ قُلْ أَرَءَيْتُمْ إِن جَعَلَ ٱللَّهُ عَلَيْكُمُ ٱلنَّهَارَ سَرْمَدًا إِلَىٰ
يَوْمِ ٱلْقِيَٰمَةِ مَنْ إِلَٰهٌ غَيْرُ ٱللَّهِ يَأْتِيكُم بِلَيْلٍ تَسْكُنُونَ
فِيهِ ۖ أَفَلَا تُبْصِرُونَ ٧٢ وَمِن رَّحْمَتِهِۦ جَعَلَ لَكُمُ ٱلَّيْلَ
وَٱلنَّهَارَ لِتَسْكُنُوا۟ فِيهِ وَلِتَبْتَغُوا۟ مِن فَضْلِهِۦ وَلَعَلَّكُمْ
تَشْكُرُونَ ٧٣ وَيَوْمَ يُنَادِيهِمْ فَيَقُولُ أَيْنَ شُرَكَآءِىَ ٱلَّذِينَ
كُنتُمْ تَزْعُمُونَ ٧٤ وَنَزَعْنَا مِن كُلِّ أُمَّةٍ شَهِيدًا فَقُلْنَا
هَاتُوا۟ بُرْهَٰنَكُمْ فَعَلِمُوٓا۟ أَنَّ ٱلْحَقَّ لِلَّهِ وَضَلَّ عَنْهُم
مَّا كَانُوا۟ يَفْتَرُونَ ٧٥ ۞ إِنَّ قَٰرُونَ كَانَ مِن قَوْمِ مُوسَىٰ الحِزْبُ
فَبَغَىٰ عَلَيْهِمْ ۖ وَءَاتَيْنَٰهُ مِنَ ٱلْكُنُوزِ مَآ إِنَّ مَفَاتِحَهُۥ لَتَنُوٓأُ
بِٱلْعُصْبَةِ أُو۟لِى ٱلْقُوَّةِ إِذْ قَالَ لَهُۥ قَوْمُهُۥ لَا تَفْرَحْ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ
لَا يُحِبُّ ٱلْفَرِحِينَ ٧٦ وَٱبْتَغِ فِيمَآ ءَاتَىٰكَ ٱللَّهُ ٱلدَّارَ ٱلْءَاخِرَةَ ۖ
وَلَا تَنسَ نَصِيبَكَ مِنَ ٱلدُّنْيَا ۖ وَأَحْسِن كَمَآ أَحْسَنَ ٱللَّهُ إِلَيْكَ ۖ
وَلَا تَبْغِ ٱلْفَسَادَ فِى ٱلْأَرْضِ ۖ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ ٱلْمُفْسِدِينَ ٧٧

**71** **Ya kai wannan Manzo ka cewa waxannan Mushirikai: "Ku bani labari, idan Allah ya mayar muku da dare ya zama dawwamamme, mai xorewa, ba ya yankewa har zuwa ranar tashin alqiyama, wane abin bauta ne koma bayan Allah wanda zai kawo muku haske irin hasken rana?!. Shi ba kwa jin waxannan hujjojin ne, ku san cewa babu wani abin bautawa koma bayan Allah da zai iya muku wannan?!.**

**72** **Ka ce da su – Ya kai wannan Manzo-: "Ku bani labari, idan Allah ya mayar da rana dawwamammiya, mai xorewa, har zuwa ranar alqiyama, wane abin bauta ne koma bayan Allah zai kawo muku daren da zaku zauna a ciki, ku huta daga wahalar aikin rana?! Shi ba kwa kallon waxannan ayoyin ne, ku san cewa babu wani abin bauta koma bayan Allah, wanda zai iya kawo waxannan gabaxayansu?!**

**73** **Yana daga cikin rahamar Allah (S.W.T) da ya sanya muku dare ya zama mai duhu, don ku huta a cikinsa, bayan abin da kuka sha na wahalar aikin rana, kuma ya sanya muku rana mai haske, don ku tafi neman arziki a cikinta, kuma domin ku godewa ni'imomin Allah a kanku, kar ku butulce masa.**

**74** **Ranar da Ubangijinsu zai kira su ya ce: "Ina abokan tarayyata da kuka kasance kuna bauta musu koma bayana, kuna riya cewa abokan tarayya ne a gare ni?!".**

**75** **Zamu halarto da Annabin kowace al'umma, domin ya bayar da shaida a kansu, na abin da suka kasance a ciki na kafirci da qaryata Manzanni, sai mu cewa masu qaryata Manzanni a cikin waxannan al'ummun: "Ku kawo hujjojinku da dalilanku na abin da kuka kasance a kai na kafirci da qaryatawa, sai hujjojinsu su yanke, su yi yaqinin cewa gaskiyar da babu shakka a cikinta ta Allah ce, Kuma duk abin da suka kasance suna qirqirarsa na abokan tarayya ga Allah sun vace, sun gushe.**

**Yayin da Allah ya ambaci cewa Fir'auna ya yi xagawa a bayan qasa, saboda mulki, sai ya ambaci xagawar Qaruna saboda dukiya, ya ce:**

**76** **Haqiqa Qaruna ya kasance daga cikin mutanen Annabi Musa (A.S) amma sai ya yi musu girman kai. Mun bashi taskokin dukiya, waxanda xaukan makullansu yana yin nauyi ga mutane masu qarfi. Yayin da mutanensa suka ce masa: "Kar ka yi farin cikin irin na alfahari, don lallai Allah ba ya son masu farin ciki na alfahari, yana fushi da su, kuma ya azabta su a kan haka".**

**77** **"Kuma ka nemi ladan gidan lahira cikin abin da Allah ya ba ka na dukiyoyi, ta hanyar ka ciyar da su cikin hanyoyin alheri, kuma kada ka manta da rabonka, na ci da sha da tufafi da sauransu, na jin daxi ba tare da almubazzaranci ko rowa ba, kuma ka kyautata mu'amala da Ubangijinka da kuma bayinsa, kamar yadda Allah ya kyautata maka, kada ka yi varna a bayan qasa, ta hanyar aikata savo da qin yin biyayya. Lallai Allah baya son masu varna a bayan qasa, yana fushi da su".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Jujjuyawar dare da rana yana daga cikin ni'imomin Allah, da ya wajaba a gode masa a kansu.**
**2 - Wuce gona da iri kamar yadda yake kasancewa da sarauta da mulki, haka ma ya kan kasance da dukiya.**
**3 - Farin ciki na alfahari savo ne, wanda Allah yake fushi da shi.**
**4 - Wajabcin yin nasiha ga wanda ake ji masa tsoron fitina.**
**5 - Fushin Allah da masu varna a bayan qasa.**

قَالَ إِنَّمَآ أُوتِيتُهُۥ عَلَىٰ عِلۡمٍ عِندِيٓۚ أَوَلَمۡ يَعۡلَمۡ أَنَّ ٱللَّهَ قَدۡ أَهۡلَكَ
مِن قَبۡلِهِۦ مِنَ ٱلۡقُرُونِ مَنۡ هُوَ أَشَدُّ مِنۡهُ قُوَّةٗ وَأَكۡثَرُ جَمۡعٗاۚ
وَلَا يُسۡـَٔلُ عَن ذُنُوبِهِمُ ٱلۡمُجۡرِمُونَ ٧٨ فَخَرَجَ عَلَىٰ قَوۡمِهِۦ
فِي زِينَتِهِۦۖ قَالَ ٱلَّذِينَ يُرِيدُونَ ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَا يَٰلَيۡتَ لَنَا
مِثۡلَ مَآ أُوتِيَ قَٰرُونُ إِنَّهُۥ لَذُو حَظٍّ عَظِيمٖ ٧٩ وَقَالَ ٱلَّذِينَ
أُوتُواْ ٱلۡعِلۡمَ وَيۡلَكُمۡ ثَوَابُ ٱللَّهِ خَيۡرٞ لِّمَنۡ ءَامَنَ وَعَمِلَ
صَٰلِحٗاۚ وَلَا يُلَقَّىٰهَآ إِلَّا ٱلصَّٰبِرُونَ ٨٠ فَخَسَفۡنَا بِهِۦ
وَبِدَارِهِ ٱلۡأَرۡضَ فَمَا كَانَ لَهُۥ مِن فِئَةٖ يَنصُرُونَهُۥ مِن دُونِ
ٱللَّهِ وَمَا كَانَ مِنَ ٱلۡمُنتَصِرِينَ ٨١ وَأَصۡبَحَ ٱلَّذِينَ تَمَنَّوۡاْ
مَكَانَهُۥ بِٱلۡأَمۡسِ يَقُولُونَ وَيۡكَأَنَّ ٱللَّهَ يَبۡسُطُ ٱلرِّزۡقَ لِمَن
يَشَآءُ مِنۡ عِبَادِهِۦ وَيَقۡدِرُۖ لَوۡلَآ أَن مَّنَّ ٱللَّهُ عَلَيۡنَا لَخَسَفَ بِنَاۖ
وَيۡكَأَنَّهُۥ لَا يُفۡلِحُ ٱلۡكَٰفِرُونَ ٨٢ تِلۡكَ ٱلدَّارُ ٱلۡأٓخِرَةُ نَجۡعَلُهَا
لِلَّذِينَ لَا يُرِيدُونَ عُلُوّٗا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَا فَسَادٗاۚ وَٱلۡعَٰقِبَةُ لِلۡمُتَّقِينَ
٨٣ مَن جَآءَ بِٱلۡحَسَنَةِ فَلَهُۥ خَيۡرٞ مِّنۡهَاۖ وَمَن جَآءَ بِٱلسَّيِّئَةِ فَلَا
يُجۡزَى ٱلَّذِينَ عَمِلُواْ ٱلسَّيِّـَٔاتِ إِلَّا مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٨٤



**(78) Sai Qaruna ya ce: "Kawai dai an ba ni waxannan dukiyoyin ne saboda wani ilimi da iko nawa dake wurina, don haka na cancanci a ba ni wannan dukiyoyin. Shin Qaruna bai da masaniyar cewa Allah ya halaka al'ummu cikin waxanda suka gabace shi, waxanda suka fi shi tsananin qarfi da yawan tara dukiya ba ne?!. Sai ga shi qarfinsu da dukiyoyinsu basu amfane su ba. Kuma ba za a tambayi masu laifin a ranar alqiyama dangane da laifukansu ba, saboda Allah ya riga ya san su, don haka tambayar da za a yi musu tambaya ce ta qurewa da tsawatarwa.**

**(79) Qaruna ya fito cikin adonsa, yana mai nuna adonsa ga mutanensa. Sai waxanda suke kwaxayin adon duniya cikin abokan Qaruna suka ce: "Ina ma da muma an ba mu kayan qawa na duniya irin yadda aka bai wa Qaruna, lallai Qaruna ma'abocin babbar rabo ne, mai yawan gaske". (80) Waxanda aka basu ilimi yayin da suka ga Qaruna a cikin ado, kuma suka ji abin da abokansa suka ce, sai su suka ce: "Kaiconku! Ladan Allah a lahira, da abin da ya tanadar na ni'ima ga waxanda suka yi imani da shi, kuma suka aikata aiki nagari, ya fi alheri sama da abin da aka bai wa Qaruna na kayan qawar rayuwar duniya. Kuma babu wanda ake yi masa dacen faxin wannan zance da aiki da abin da ya qunsa, sai masu haquri, waxanda suke yin haqurin fifita abin da ke wurin Allah na lada a kan abin da ke cikin duniya na jin daxi mai gushewa".**

**(81) Sai muka kifar da shi da gidansa a cikin qasa, da duk wanda suke cikin gidan, azaba a gare shi, saboda zaluncinsa. Sai ya kasance ba shi da wasu jama'a da zasu taimake shi koma bayan Allah, kuma bai kasance cikin wanxanda za su iya taimaka wa kawunansu da kansu ba.**

**(82) sai waxanda suka kasance suna burin abin da yake da shi na dukiya da ado kafin a kife shi suka wayi gari suna cewa, cikin baqin ciki da la'akari da abin da ya faru da shi: "Ashe ba mu san cewa Allah ne yake yalwata arziki ga wanda ya ga dama daga cikin bayinsa ba, kuma ya quntata shi ga wanda ya ga dama a cikinsu?! Ba domin Allah ya yi mana ni'ima ba, bai kama mu da laifin abin da muka faxa ba, ai da mu ma an kife mu, kamar yadda aka kife Qaruna. Lallai kafirai ba sa rabauta, a duniya ko a lahira. qarshen lamarinsu da makomarsu ita ce hasara a cikinsu.**

**(83) Wancan gidan Lahirar, muna sanya shi ya zama gidan ni'ima da girmamawa ga waxanda ba sa nufin girman kai a bayan qasa, su qi yin imani da gaskiya da bin sa, kuma ba sa nufin varna a cikinta. Makoma abin yabo ita ce abin da yake cikin Aljanna na ni'imomi, da abin da zai sauka a cikinta na yardar Allah ga masu jin tsoron Ubangijinsu, ta hanyar bin umarninsa da nesantar abin da ya hana.**

**(84) Duk wanda ya zo da kyakkyawan aiki a ranar Lahira – na sallah da zakka da azimi da sauransu- to yana da sakamako wanda ya fi wancan kyakkyawan aikin, ta yadda za a ruvanya masa ladan aiki guda xaya zuwa ninki goma irinsa. Kuma duk wanda ya zo ranar alqiyama da mummunan aiki –na kafirci da cin kuxin ruwa da zina da sauransu- to babu abin da za a sakawa waxanda suka munana aiki da shi sai dai irin abin da suka aikata, babu qari.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Duk abin da yake tare da mutum na alheri da ni'imomi, to daga wurin Allah yake, halittarsa ne da qaddarawarsa.**
**2 - Ma'abota ilimi su ne ma'abota hikima, masu kuvuta daga fitintinu, saboda ilimi yana shiryar da ma'abocinsa zuwa daidai. 3 - xaukaka da girman kai a bayan qasa da yaxa varna, qarshensa halaka ne da hasara.**
**4 - Yalwan rahamar Allah da adalcinsa na ruvanya ladan kyawawan ayyuka ga Mumini da rashin ruvanya mummuna ga kafiri.**

(85) **Lallai wanda ya saukar maka da Alqur'ani, kuma ya wajabta maka isar da shi, da aiki da abin da yake cikin sa, shi ne wanda zai dawo da kai garin Makkah, ka buxe ta cikin nasara. Ka ce wa Mushirikai - ya kai wannan Manzo -: "Ubangijina shi ya fi sanin wane ne ya zo da shiriya, kuma wane ne yake cikin vata mabayyani, nesa da shiriya da gaskiya". (86) Kuma – Ya kai wannan Manzo- ba ka kasance ba kafin a turo ka, kana fatan a saukar maka da Alqur'ani a matsayin wahayi daga Allah. Sai dai kawai rahama ce daga wurin Allah ta hukunta saukar da shi a gare ka. Saboda haka kada ka zama mai taimakawa kafirai a kan abin da suke a kai na vata. (87) Kada waxannan Mushirikai su kawar da kai daga ayoyin Allah, bayan an sauka maka da su, har ka daina karanta su, da isar da su. Kuma ka kira mutane zuwa imani da Allah, da qaxaita shi, da aiki da shari'arsa. Kuma kada ka kasance cikin Mushirikai, waxanda suke bautawa wanin Allah tare da shi. Ka kasance cikin masu tauhidi, waxanda ba sa bautawa kowa sai Allah shi kaxai. (88) Kuma kada bauta wa wani abin bauta tare da Allah, babu wani abin bauta bisa cancanta bayan shi. Komai mai halaka ne ban da Fuskarsa, tsarki ya tabbata a gare shi. Shi kaxai yake da hukunci, yana hukunci da abin da ya ga dama, kuma zuwa gare shi, shi kaxai za a mayar da ku a ranar alqiyama, domin hisabi da sakamako.**

إِنَّ ٱلَّذِي فَرَضَ عَلَيۡكَ ٱلۡقُرۡءَانَ لَرَآدُّكَ إِلَىٰ مَعَادٖۚ قُل رَّبِّيٓ
أَعۡلَمُ مَن جَآءَ بِٱلۡهُدَىٰ وَمَنۡ هُوَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ٨٥ وَمَا كُنتَ
تَرۡجُوٓاْ أَن يُلۡقَىٰٓ إِلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبُ إِلَّا رَحۡمَةٗ مِّن رَّبِّكَۖ فَلَا
تَكُونَنَّ ظَهِيرٗا لِّلۡكَٰفِرِينَ ٨٦ وَلَا يَصُدُّنَّكَ عَنۡ ءَايَٰتِ
ٱللَّهِ بَعۡدَ إِذۡ أُنزِلَتۡ إِلَيۡكَۖ وَٱدۡعُ إِلَىٰ رَبِّكَۖ وَلَا تَكُونَنَّ مِنَ
ٱلۡمُشۡرِكِينَ ٨٧ وَلَا تَدۡعُ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَۘ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۚ
كُلُّ شَيۡءٍ هَالِكٌ إِلَّا وَجۡهَهُۥۚ لَهُ ٱلۡحُكۡمُ وَإِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ٨٨

آياتها ٦٩ — سُورَةُ العَنكَبُوت — ترتيبها ٢٩

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الٓمٓ ١ أَحَسِبَ ٱلنَّاسُ أَن يُتۡرَكُوٓاْ أَن يَقُولُوٓاْ ءَامَنَّا وَهُمۡ نصف الحزب ٤٠
لَا يُفۡتَنُونَ ٢ وَلَقَدۡ فَتَنَّا ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۖ فَلَيَعۡلَمَنَّ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ
صَدَقُواْ وَلَيَعۡلَمَنَّ ٱلۡكَٰذِبِينَ ٣ أَمۡ حَسِبَ ٱلَّذِينَ يَعۡمَلُونَ
ٱلسَّيِّـَٔاتِ أَن يَسۡبِقُونَاۚ سَآءَ مَا يَحۡكُمُونَ ٤ مَن كَانَ يَرۡجُواْ
لِقَآءَ ٱللَّهِ فَإِنَّ أَجَلَ ٱللَّهِ لَأٓتٖۚ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٥ وَمَن
جَٰهَدَ فَإِنَّمَا يُجَٰهِدُ لِنَفۡسِهِۦٓۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَغَنِيٌّ عَنِ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٦



# Suratul Ankabut

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Ta bayar da muhimmanci a kan tabbata da haquri a yayin jarabawa da fitintinu, da kuma bayanin fitintinun da zasu kasance da qarshensu.**

## Tafsir:

(1) **(Alif Laam Mim): Bayani ya gabata a kan ire-iren waxannan haruffa a farkon Suratul Baqara.**
(2) **Shin mutane suna zaton shi kenan don sun ce: "Mun yi imani da Allah" sai a qyale su, ba tare da jarabawar da zata bayyana haqiqanin abin da suka faxa ba, cewa: "Shin su Muminai ne da gaske ba?!" Abin ba kamar yadda suke zato ba ne.**
(3) **Haqiqa mun jarraba waxanda suke a gabaninsu. Da sannu Allah zai bayyana ya yaye muku gaskiyar masu gaskiya a cikin imaninsu, da qaryar masu qarya a ciki.**
(4) **Bari dai, shin waxanda suke aikata savo na shirka da waninsa, suna zaton cewa za su tsere mana ne, su kuvuta daga uqubarmu?! Tir da wannan hukuncin na su da suke hukunci da shi!. Su baza su gagari Allah ba, kuma baza su tsira daga uqubarsa ba, in sun mutu a kan kafircinsu.**
(5) **Duk wanda yake fatan saduwa da Allah a ranar alqiyama don ya ba shi lada, to ya sani cewa ajalin da Allah ya sanya na yin hakan yana nan zuwa, nan kusa. Kuma Shi Allah mai jin zancen bayinsa ne, Masanin ayyukansu ne. Babu abin da yake kuvuce masa a ciki, kuma da sannu zai yi musu sakayya a kansu.**
(6) **Duk wanda ya yi fama da ransa, ya xora zuciyarsa a kan xa'a da nesantar savo, kuma ya yi jihadi don xaukaka Kalmar Allah, to jihadinsa don kansa ya yi wa, domin amfanin hakan yana komawa ne zuwa gare shi. Allah mawadaci ne daga barin talikai gaba xayansu, don haka xa'arsu bata qara mishi komai, haka ma savonsu baya rage shi da komai.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** 1 - **Hani a kan taimakon ma'abota vata.** 2 - **Umarni da riqo da kaxaita Allah da nesantar shirka da shi.** 3 - **Jarraba Muminai da bala'o'i sunna ce ta Allah.** 4 - **Wadatuwar Allah da rashin buqatarsa ga biyayyar bayinsa.**

وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَنُكَفِّرَنَّ عَنۡهُمۡ سَيِّـَٔاتِهِمۡ
وَلَنَجۡزِيَنَّهُمۡ أَحۡسَنَ ٱلَّذِي كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٧ وَوَصَّيۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ
بِوَٰلِدَيۡهِ حُسۡنٗاۖ وَإِن جَٰهَدَاكَ لِتُشۡرِكَ بِي مَا لَيۡسَ لَكَ بِهِۦ عِلۡمٞ
فَلَا تُطِعۡهُمَآۚ إِلَيَّ مَرۡجِعُكُمۡ فَأُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ٨
وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ لَنُدۡخِلَنَّهُمۡ فِي ٱلصَّٰلِحِينَ
٩ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَقُولُ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ فَإِذَآ أُوذِيَ فِي ٱللَّهِ جَعَلَ
فِتۡنَةَ ٱلنَّاسِ كَعَذَابِ ٱللَّهِۖ وَلَئِن جَآءَ نَصۡرٞ مِّن رَّبِّكَ لَيَقُولُنَّ
إِنَّا كُنَّا مَعَكُمۡۚ أَوَلَيۡسَ ٱللَّهُ بِأَعۡلَمَ بِمَا فِي صُدُورِ ٱلۡعَٰلَمِينَ
١٠ وَلَيَعۡلَمَنَّ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَلَيَعۡلَمَنَّ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ
١١ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لِلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّبِعُواْ سَبِيلَنَا
وَلۡنَحۡمِلۡ خَطَٰيَٰكُمۡ وَمَا هُم بِحَٰمِلِينَ مِنۡ خَطَٰيَٰهُم مِّن
شَيۡءٍۖ إِنَّهُمۡ لَكَٰذِبُونَ ١٢ وَلَيَحۡمِلُنَّ أَثۡقَالَهُمۡ وَأَثۡقَالٗا مَّعَ
أَثۡقَالِهِمۡۖ وَلَيُسۡـَٔلُنَّ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ عَمَّا كَانُواْ يَفۡتَرُونَ
١٣ وَلَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا نُوحًا إِلَىٰ قَوۡمِهِۦ فَلَبِثَ فِيهِمۡ أَلۡفَ سَنَةٍ
إِلَّا خَمۡسِينَ عَامٗا فَأَخَذَهُمُ ٱلطُّوفَانُ وَهُمۡ ظَٰلِمُونَ ١٤



**(7) Waxanda suka yi imani, suka yi haquri a kan jarrabawarmu a gare su, kuma suka aikata kyawawan aiki, to zamu share musu zunubbansu da abin da suka aikata na kyawawan ayyuka, kuma lallai zamu saka musu a lahira da mafi kyan abin da suka kasance suna aikatawa a duniya.**

**(8) Mun yi wa mutum wasiyya dangane da iyayen shi cewa ya kyautata musu. Kuma idan iyayenka guda biyun – Ya kai mutum- sun yi qoqari su ja ka, don ka haxa ni da abin da baka da masaniyar cewa abokin tarayya ne a gare ni – kamar yadda ya faru ga Sa'adu xan Abi Waqqas (R.A) daga mahaifiyarsa- ta kada ka yi musu xa'a a cikin wannan, saboda ba a yin xa'a ga abin halitta cikin savon Mahalicci. Zuwa gare ni ne ni kaxai makomarku take a ranar alqiyama, sai in baku labarin abin da kuka kasance kuna aikatawa, kuma in saka muka a kai.**

**(9) Waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka aikata kyawawan ayyuka, to lallai zamu shigar da su cikin bayi nagartattu a ranar alqiyama, mu tara su tare da su, mu basu lada irin na su.**

**(10) A cikin mutane akwai wanda yake cewa: “Mun yi imani da Allah, amma da zarar kafirai sun cutar da shi, saboda imaninsa, sai ya xauki cutarwar kafirai kamar azabar Allah ce, sai ya yi ridda ya bar imani, don ya dace da kafirai. Kuma idan nasara ta faru gare ka daga Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo- sai su ce: “Ai lallai da man muna tare da ku – Ya ku Muminai- a kan imani”. Shin Allah ba shi ba ne mafi sanin abin da yake cikin zukatan mutane ba?! Babu abin da yake vuya gare shi na kafirci da imanin dake cikinsu. To ta yaya zasu ba Allah labarin abin da ke zukatansu alhali shi ya fi su sanin abin da yaka ciki zukatan na su?!.**

**(11) Kuma tabbas sai Allah ya bayyana saninsa na waxandan suka yi imani da shi na gaskiya. Kuma tabbas sai ya bayyana saninsa na Munafikai waxanda suka nuna imani a zahiri, kuma suka voye kafirci a zukatansu.**

**(12) Waxanda suka kafirta suka ce wa waxanda suka yi imani da Allah shi kaxai: “Ku bi addininmu da abin da muke kai, mu zamu xauke muku zunubanku a madadinku, sai a ba mu sakamakonsu banda ku”, alhali babu wani abu na zunubansu da za su xauke musu, kuma lallai su qarya suke a cikin wannan zancen na su.**

**Yayin da kore xaukan laifin wasunsu zai iya sa a fahimci cewa, kafirai masu kira zuwa ga vatan da suke kai, ba za a xora musu wani laifi a kan laifinsu ba, sai Allah ya kawar da wannan fahimta ya ce:**

**(13) Waxannan Mushirika masu kira zuwa ga varnarsu zasu xauki zunuban laifukan da suka yi, da zunuban laifukan waxanda suka bi kiransu, ba tare da an rage wani abu daga cikin zunuban waxanda suka yi musu biyayya ba. Kuma tabbas sai an tambaye su a ranar alqiyama dangane da abin da suka kasance suna qirqira na qareraki a duniya.**

**(14) Haqiqa mun aika Annabi Nuhu a matsayin Manzo zuwa ga mutanensa, ya zauna a cikinsu shekara xari tara da hamsin, yana kiransu zuwa ga kaxaita Allah, sai suka qaryata shi, suka xore a kan kafircinsu, sai ruwan Xufana ya kama su, suna azzalumai, saboda kafircinsu da Allah, da qaryatawarsu da Manzanni, aka halakar da su da nutsewa a cikin ruwa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Allah yana kankare zunubai da kyawawan ayyuka.**

**2 - Karfafa wajabcin kyautata wa iyaye.**

**3 - Imani da Allah yana wajabta yin haquri da cutarwa a ka tafarkinsa.**

**4 - Duk wanda ya farar da wani mummunan tsari, to yana da laifinsa, da laifukan duk wanxanda suka yi koyi da shi, ba tare da an rage komai cikin laifukansu ba.**

فَأَنجَيۡنَٰهُ وَأَصۡحَٰبَ ٱلسَّفِينَةِ وَجَعَلۡنَٰهَآ ءَايَةٗ لِّلۡعَٰلَمِينَ
١٥ وَإِبۡرَٰهِيمَ إِذۡ قَالَ لِقَوۡمِهِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱتَّقُوهُۖ ذَٰلِكُمۡ
خَيۡرٞ لَّكُمۡ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ١٦ إِنَّمَا تَعۡبُدُونَ مِن
دُونِ ٱللَّهِ أَوۡثَٰنٗا وَتَخۡلُقُونَ إِفۡكًاۚ إِنَّ ٱلَّذِينَ تَعۡبُدُونَ مِن
دُونِ ٱللَّهِ لَا يَمۡلِكُونَ لَكُمۡ رِزۡقٗا فَٱبۡتَغُواْ عِندَ ٱللَّهِ ٱلرِّزۡقَ
وَٱعۡبُدُوهُ وَٱشۡكُرُواْ لَهُۥٓۖ إِلَيۡهِ تُرۡجَعُونَ ١٧ وَإِن تُكَذِّبُواْ
فَقَدۡ كَذَّبَ أُمَمٞ مِّن قَبۡلِكُمۡۖ وَمَا عَلَى ٱلرَّسُولِ إِلَّا ٱلۡبَلَٰغُ
ٱلۡمُبِينُ ١٨ أَوَلَمۡ يَرَوۡاْ كَيۡفَ يُبۡدِئُ ٱللَّهُ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ
يُعِيدُهُۥٓۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٞ ١٩ قُلۡ سِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ
فَٱنظُرُواْ كَيۡفَ بَدَأَ ٱلۡخَلۡقَۚ ثُمَّ ٱللَّهُ يُنشِئُ ٱلنَّشۡأَةَ ٱلۡأٓخِرَةَۚ
إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٢٠ يُعَذِّبُ مَن يَشَآءُ وَيَرۡحَمُ
مَن يَشَآءُۖ وَإِلَيۡهِ تُقۡلَبُونَ ٢١ وَمَآ أَنتُم بِمُعۡجِزِينَ فِي
ٱلۡأَرۡضِ وَلَا فِي ٱلسَّمَآءِۖ وَمَا لَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ مِن
وَلِيّٖ وَلَا نَصِيرٖ ٢٢ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ وَلِقَآئِهِۦٓ
أُوْلَٰٓئِكَ يَئِسُواْ مِن رَّحۡمَتِي وَأُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ ٢٣



**(15) Sai muka tserar da Annabi Nuhu daga halakar nutsewa da Muminan da suke tare da shi a cikin jirgin ruwa, kuma muka sanya jirgin ruwan ya zama abin izna ga mutane, suna la'akari da shi.**

**(16) Ya kai wannan Manzo- ka ambaci qissar Annabi Ibrahim yayin da ya cewa mutanensa: "Ku bauta wa Allah shi kaxai, ku ji tsoron uqubarsa, ta hanyar bin umarninsa, da nesantar haninsa. Wannan abin da aka yi muku umarni da shi, shi ne mafi alheri a gare ku, in kun kasance kuna da sani".**

**(17) Ba wani abu kuke bauta wa ba –Ya ku Mushirikai- face gumakan da ba sa amfanar wa ko cutarwa, kuma qirqirar qarya kuke yi yayin da kuke riya cancantarsu da bauta. Lallai waxanda kuke bautawa koma bayan Allah, ba su da ikon azurta ku, ballantana su azurta ku. Don haka ku nemi arziki a wurin Allah kawai, domin shi ne mai azurtawa, kuma ku bauta masa shi kaxai, ku gode masa abin da ya yi muku na ni'mar arziki. Zuwa gare shi, shi kaxai za a mayar da ku ranar alqiyama don hisabi da sakamako, ba zuwa ga gumakanku ba.**

**(18) Ya ku mushirikai- idan kuka qaryata abin da Annabi Muhammad (S.A.W) ya zo da shi, to al'ummun da suka gabaceku sun qaryata Manzanni, irin su mutanen Annabi Nuhu da Adawa da Samudawa. Babu abin da ya wajaba a kan manzo face isarwa mabayyaniya. Kuma alal-haqiqa ya isar muku da abin da Ubangijinsa ya umurce shi ya isar muku da shi.**

**(19) Shin waxannan masu qaryata Manzanni basu ga yaya Allah ya fara halittar halittu da farko ba, sannan kuma ya mayar da su bayan sun gushe ba?! Lallai wannan abu ne mai sauki a wurin Allah. Shi mai iko ne, babu abin da yake gagarar shi.**

**(20) Ka faxa wa waxannan masu qaryata tashin Alqiyama - Ya kai wannan Manzo- cewa: "ku yi tafiya a bayan qasa, ku kalli yadda Allah ya fari halitta, sannan kuma Allah shi ne yake rayar da mutane bayan mutuwarsu, rayuwa ta biyu, domin tashi da hisabi. Lallai Allah mai iko ne a kan komai. Babu abin da yake gagararsa. Don haka ba zai kasa tayar da mutane ba, kamar yadda bai kasa halittarsu da farko ba.**

**(21) Ya na azabta wanda ya ga dama daga cikin halittarsa da adalcinsa, kuma ya na jin qan wanda ya ga dama daga cikin halittarsa da falalarsa. Kuma gare shi ne, shi kaxai za a mayar da ku a ranar alqiyama, don yi muku hisabi, a yayin da zai tayar da ku, daga qaburburanku kuna rayayyu.**

**(22) Kuma ba zaku kuvuce wa Ubangijinku ba, ba zaku kuvuta daga uqubarsa ba a bayan qasa ko a sama. Ba ku da wani majivinjin lamari wanda zai jivinci lamarinku, koma bayan Allah, Kuma baku da wani mai taimako koma bayan Allah, wanda zai xauke muku azabarsa.**

**(23) Waxanda suka kafirce wa Allah, da ayoyin Allah mai tsarki, da saduwa da shi a ranar alqiyama, su ne waxanda suka xebe qauna daga rahamata, don haka ba zasu shiga Aljanna ba har abada, saboda kafircinsu, Kuma waxannan suna da azaba mai raxaxi, wadda take jiransu a lahira.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Gumaka ba su da ikon azurtawa, don haka ba su cancanci bauta ba.**
**2 - Ana neman arziki ne a wurin Allah, wanda yake mallakar arziki.**
**3 - Fara halitta dalili ne a kan yiwuwar tashin bayan mutuwa.**
**4 - Shiga Aljanna ba zai yiwu ba ga wanda ya mutu a kan kafircinsa.**

فَمَا كَانَ جَوَابَ قَوْمِهِۦٓ إِلَّآ أَن قَالُواْ ٱقْتُلُوهُ أَوْ حَرِّقُوهُ
فَأَنجَىٰهُ ٱللَّهُ مِنَ ٱلنَّارِ ۚ إِنَّ فِى ذَٰلِكَ لَءَايَٰتٍ لِّقَوْمٍ يُؤْمِنُونَ
٢٤ وَقَالَ إِنَّمَا ٱتَّخَذْتُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ أَوْثَٰنًا مَّوَدَّةَ بَيْنِكُمْ
فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا ۖ ثُمَّ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ يَكْفُرُ بَعْضُكُم
بِبَعْضٍ وَيَلْعَنُ بَعْضُكُم بَعْضًا وَمَأْوَىٰكُمُ ٱلنَّارُ
وَمَا لَكُم مِّن نَّٰصِرِينَ ٢٥ ۞ فَـَٔامَنَ لَهُۥ لُوطٌ ۘ وَقَالَ
إِنِّى مُهَاجِرٌ إِلَىٰ رَبِّىٓ ۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ ٢٦
وَوَهَبْنَا لَهُۥٓ إِسْحَٰقَ وَيَعْقُوبَ وَجَعَلْنَا فِى ذُرِّيَّتِهِ
ٱلنُّبُوَّةَ وَٱلْكِتَٰبَ وَءَاتَيْنَٰهُ أَجْرَهُۥ فِى ٱلدُّنْيَا ۖ وَإِنَّهُۥ
فِى ٱلْءَاخِرَةِ لَمِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ٢٧ وَلُوطًا إِذْ قَالَ لِقَوْمِهِۦٓ
إِنَّكُمْ لَتَأْتُونَ ٱلْفَٰحِشَةَ مَا سَبَقَكُم بِهَا مِنْ أَحَدٍ
مِّنَ ٱلْعَٰلَمِينَ ٢٨ أَئِنَّكُمْ لَتَأْتُونَ ٱلرِّجَالَ وَتَقْطَعُونَ
ٱلسَّبِيلَ وَتَأْتُونَ فِى نَادِيكُمُ ٱلْمُنكَرَ ۖ فَمَا كَانَ جَوَابَ
قَوْمِهِۦٓ إِلَّآ أَن قَالُواْ ٱئْتِنَا بِعَذَابِ ٱللَّهِ إِن كُنتَ مِنَ
ٱلصَّٰدِقِينَ ٢٩ قَالَ رَبِّ ٱنصُرْنِى عَلَى ٱلْقَوْمِ ٱلْمُفْسِدِينَ ٣٠

ثلاثة أرباع الحزب ٤٠



**(24) Babu abin da ya kasance amsar mutanen Annabi Ibrahim (A.S) bayan ya umurce su da bautawa Allah shi kaxai, da barin bautar waninsa daga gumaka- face kawai sun cewa junansu: "ku kashe shi, ko ku jefa shi a wuta, don bayar da kariya ga abubuwan bautarku". Sai Allah ya kuvutar da shi daga wuta. Lallai a cikin kuvutar da shi daga wutar nan, bayan an jefa shi a cikinta, akwai abin izna ga mutanen da suke da imani, don su ne waxanda suke amfana da abubawan xaukan izna.**

**(25) Annabi Ibrahim (A.S) ya ce wa mutanensa: "Kawai fa kun xauki gumaka a matsayin abubuwan bauta ne, kuna bauta musu, saboda sanayya da soyayya a kan bautarsu da take tsakaninku a rayuwar duniya, sannan kuma a ranar alqiyama wannan soyayyar zata yanke a tsakaninku, sai sashenku su yi baran-baran da sashe, yayin da zaku yi ido huxu da azaba, kuma sashenku ya la'anci sashe. Kuma matabbatarku da zaku koma zuwa gare ta, ita ce wuta. Ba ku da wasu mataimaka waxanda zasu kare muku azabar Allah, a cikin gumakanku da kuka kasance kuna bautawa koma bayan Allah, ko kuma daga waninsu.**

**(26) Sai Annabi Luxu (A.S) ya yi imani da shi. Annabi Ibrahim (A.S) ya ce: "Lallai zan yi hijira zuwa ga Ubangijina in tafi qasar Sham mai albarka. Lallai Allah shi ne Mabuwayi, wanda ba a galaba a kansa, kuma duk wanda ya yi hijira zuwa gare shi, baya qasqanta, mai hikima cikin qaddarawarsa da gudanarwarsa.**

**(27) Mun ba wa Annabi Ibrahim kyautar (A.S) Annabi Is'haqa, da xansa Annabi Yaqubu (A.S), muka saka Annabci a cikin 'ya'yansa, da littafan da aka saukar da su daga wurin Allah, kuma muka ba shi ladan haqurinsa a kan gaskiya a duniya, ta hanyar gyara masa 'ya'yansa da bashi kyakyawan yabo. Kuma shi a Lahira za a ba shi sakamako irin na nagartattun bayi, abin da aka ba shi a duniya ba zai rage abin da aka yi masa tanadinsa na babban sakamako a lahira ba.**

**(28) Ya kai wannan Manzo- ka ambaci Annabi Luxu (A.S) yayin da ya cewa mutanensa: "Lallai kuna aikata mummunan zunubi irin wanda babu wanda ya riga ku aikata shi cikin talikai kafin ku, ku ne waxanda kuka fara qirqiro wannan zunubin da ya savawa kyawawan xabi'un halittar Allah.**

**(29) Haqiqa ku, kuna zakkewa maza ta duburarsu, don biyan buqatan sha'awarku, kuma kuna tare hanyar matafiya, ku hana su tafiya, saboda tsoron abin da kuke aikatawa na alfasha, kuma kuna aikata munanan ayyuka a majalisunku, irin su tsiraici da da cutar da wanda ya zo wucewa ta inda kuke, da magana ko da aiki? Babu abin da ya zama amsar mutanensa a gare shi, bayan ya hana su aikata abubuwan qyama, face abin da suka faxa masa cewa: "Ka kawo mana azabar Allah, da kake mana gargaxinta in har kana da gaskiya cikin abin da ka ke iqrarinsa".**

**(30) Sai Annabi Lux (A.S) ya ce, yana mai roqon Ubangijinsa, bayan taurin kan mutanensa, da neman da suka yi na ya sauko musu da azaba, saboda izgili da rainin hankali a gare shi: "Ya Ubangijina ka ba ni nasara a kan mutanen da suka kasance mavarnata a bayan qasa, da abin da suke yaxawa na kafirci da mummunan savo".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Kulawar Allah ga bayinsa nagari, ta yadda ya ke kuvutar da su daga makircin maqiyansu.**
**2 - Falalar yin hijira zuwa ga Allah.**
**3 - Girman matsayin Annabi Ibrahim (A.S) da iyalansa a wurin Allah Maxaukaki**
**4 - Gaggauta bayar da wani sashe na lada a duniya ba ya nufin tawayar lada a Lahira.**
**5 - Munin aikata munanan aiki a majalisu na gama gari.**

وَلَمَّا جَآءَتۡ رُسُلُنَآ إِبۡرَٰهِيمَ بِٱلۡبُشۡرَىٰ قَالُوٓاْ إِنَّا مُهۡلِكُوٓاْ
أَهۡلِ هَٰذِهِ ٱلۡقَرۡيَةِۖ إِنَّ أَهۡلَهَا كَانُواْ ظَٰلِمِينَ ٣١
قَالَ إِنَّ فِيهَا لُوطٗاۚ قَالُواْ نَحۡنُ أَعۡلَمُ بِمَن فِيهَاۖ لَنُنَجِّيَنَّهُۥ
وَأَهۡلَهُۥٓ إِلَّا ٱمۡرَأَتَهُۥ كَانَتۡ مِنَ ٱلۡغَٰبِرِينَ ٣٢ وَلَمَّآ
أَن جَآءَتۡ رُسُلُنَا لُوطٗا سِيٓءَ بِهِمۡ وَضَاقَ بِهِمۡ ذَرۡعٗاۖ
وَقَالُواْ لَا تَخَفۡ وَلَا تَحۡزَنۡ إِنَّا مُنَجُّوكَ وَأَهۡلَكَ إِلَّا
ٱمۡرَأَتَكَ كَانَتۡ مِنَ ٱلۡغَٰبِرِينَ ٣٣ إِنَّا مُنزِلُونَ عَلَىٰٓ أَهۡلِ
هَٰذِهِ ٱلۡقَرۡيَةِ رِجۡزٗا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ بِمَا كَانُواْ يَفۡسُقُونَ
٣٤ وَلَقَد تَّرَكۡنَا مِنۡهَآ ءَايَةَۢ بَيِّنَةٗ لِّقَوۡمٖ يَعۡقِلُونَ
٣٥ وَإِلَىٰ مَدۡيَنَ أَخَاهُمۡ شُعَيۡبٗا فَقَالَ يَٰقَوۡمِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ
وَٱرۡجُواْ ٱلۡيَوۡمَ ٱلۡأٓخِرَ وَلَا تَعۡثَوۡاْ فِي ٱلۡأَرۡضِ مُفۡسِدِينَ
٣٦ فَكَذَّبُوهُ فَأَخَذَتۡهُمُ ٱلرَّجۡفَةُ فَأَصۡبَحُواْ فِي دَارِهِمۡ
جَٰثِمِينَ ٣٧ وَعَادٗا وَثَمُودَاْ وَقَد تَّبَيَّنَ لَكُم
مِّن مَّسَٰكِنِهِمۡۖ وَزَيَّنَ لَهُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ أَعۡمَٰلَهُمۡ
فَصَدَّهُمۡ عَنِ ٱلسَّبِيلِ وَكَانُواْ مُسۡتَبۡصِرِينَ ٣٨



**(31) Yayin da Mala'ikun da muka aiko su, su yi wa Annabi Ibrahim (A.S) albishirin samun Annabi Is'haqa da xansa Annabi Yaqubu a bayansa, sai suka ce masa: "Haqiqa zamu halaka mutanen garin Sadum, garin mutanen Annabi Lux (A.S), domin tabbas mutanen garin sun kasance azzalumai, saboda abin da suke aikatawa na alfasha".**

**(32) Sai Annabi Ibrahim (A.S) ya ce: "Akwai Annabi Lux a cikin wannan garin da kuke son ku halaka mutanensa, kuma shi ba ya cikin azzalumai xin". Sai Malai'ikun saka ce: "Mun fi ka sanin mutanen da suke cikin ta. Zamu kuvutar da shi da iyalansa daga azabar da za a saukar a kan mutanen garin, sai matarsa kaxai, ita ta kasance tare da sauran halakakkun, don haka zamu halakata tare da su".**

**(33) Yayin da Mala'ikun da muka turo su don su halaka mutanen Annabi Luxu suka iso wurin Annabi Luxu, sai bai ji daxin zuwansu ba, ya yi baqin ciki, saboda tsoron da yake ji musu na rashin kirkin mutanensa, domin Mala'ikun sun zo masa ne a kamannin maza, kuma mutanensa suna zakke wa maza ne a madadin mata, don biyan buqatar sha'awarsu. Sai Mala'ikun suka ce masa: "Kar ka ji tsoro, mutanenka ba zasu iya isowa wajenka da wani mummunan abu ba, kuma kar ka ka yi baqin cikin abin da muka ba ka labarinsa na halaka su. Lallai zamu kuvutar da kai da iyalanka daga halakar, sai dai matarka kawai, ta kasance tare da sauran halakakkun, don haka zamu halakata tare da su.**

**(34) Zamu saukar da azaba daga sama a kan mutanen wannan gari, waxanda suka kasance suna aikata munanan ayyuka, azabar ita ce duwatsu na tavo, don ya zama uquba a gare su, saboda fitarsu daga biyayyar Allah, da abin da suke aikatawa na mummunan alfasha, wadda ita ce zakkewa maza da sha'awa a madadin mata.**

**(35) Haqiqa mun bar wata alama bayyananniya a cikin wannan gari da muka halaka shi, saboda mutane masu hankali, don su ne suke xaukan izna da ayoyi.**

**(36) Mun aikawa mutanen Madyana xan uwansu a nasaba Annabi Shu'aibu (A.S) sai ya ce: "Ya ku mutanena, ku bauta wa Allah shi kaxai, ku yi fatan kyakkyawan sakamako a lahira da bautarku gare shi, shi kaxai, kuma kada ku yi varna a bayan qasa da aikata savo da yaxa shi".**

**(37) Sai mutanensa suka qaryata shi, sai girgizar qasa ta faxa a kansu, suka wayi gari a gidansu suna faxuwa akan fuskokinsu, turvaya ta rufe fuskokinsu, ba sa iya motsi.**

**(38) Haka ma mun halaka Adawa, mutanen Annabi Hudu, da Samudawa mutanen Annabi Salihu. Kuma tabbas ta bayyana a gare ku – Ya ku mutanen Makkah- daga wuraren zamansu a garin Hijir da garin Shihri da garin Hadramauta, abin da zai nuna muku yadda aka halaka su. Gidanjen nasu babu kowa a cikinsu, suna bayar da shaida a kan hakan. Shaixan kuma ya qawata musu ayyukan su, waxanda suka kasance a kansu na kafirci da waninsa na savo, sai ya kawar da su daga tafarki madaidaici, alhali sun kasance masu basirar gane gaskiya da qarya, da shiriya da vata ta hanyar abin da Manzanninsu suka sanar da su, amma sai suka zavi bin son zuciya a kan bin gaskiya.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Faxin Allah cewa (Kuma haqiqa ta bayyana ...) yana nuna cewa Larabawa sun san gidajensu da labarinsu.**
**2 - Dangatakar dake tsakanin mutane bata amfani sai in da imani.**
**3 - Yin qoqarin bayar da kariya ga baqi da kuvutar da su daga yi musu ta'ddaci.**
**4 - Wuraren zaman waxanda aka halakar da su da azaba, abin izna ne ga masu xaukan wa'azi.**
**5 - Sanin gaskiya ba ya amfani tare da bin son zuciya da fifita shi a kan shiriya.**

وَقَٰرُونَ وَفِرۡعَوۡنَ وَهَٰمَٰنَۖ وَلَقَدۡ جَآءَهُم مُّوسَىٰ بِٱلۡبَيِّنَٰتِ
فَٱسۡتَكۡبَرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَمَا كَانُواْ سَٰبِقِينَ ٣٩
فَكُلًّا أَخَذۡنَا بِذَنۢبِهِۦۖ فَمِنۡهُم مَّنۡ أَرۡسَلۡنَا عَلَيۡهِ حَاصِبٗا
وَمِنۡهُم مَّنۡ أَخَذَتۡهُ ٱلصَّيۡحَةُ وَمِنۡهُم مَّنۡ خَسَفۡنَا بِهِ
ٱلۡأَرۡضَ وَمِنۡهُم مَّنۡ أَغۡرَقۡنَاۚ وَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيَظۡلِمَهُمۡ
وَلَٰكِن كَانُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ٤٠ مَثَلُ ٱلَّذِينَ
ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَوۡلِيَآءَ كَمَثَلِ ٱلۡعَنكَبُوتِ
ٱتَّخَذَتۡ بَيۡتٗاۖ وَإِنَّ أَوۡهَنَ ٱلۡبُيُوتِ لَبَيۡتُ ٱلۡعَنكَبُوتِۚ
لَوۡ كَانُواْ يَعۡلَمُونَ ٤١ إِنَّ ٱللَّهَ يَعۡلَمُ مَا يَدۡعُونَ مِن
دُونِهِۦ مِن شَيۡءٖۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٤٢ وَتِلۡكَ
ٱلۡأَمۡثَٰلُ نَضۡرِبُهَا لِلنَّاسِۖ وَمَا يَعۡقِلُهَآ إِلَّا ٱلۡعَٰلِمُونَ
٤٣ خَلَقَ ٱللَّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ بِٱلۡحَقِّۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ
لَأٓيَةٗ لِّلۡمُؤۡمِنِينَ ٤٤ ٱتۡلُ مَآ أُوحِيَ إِلَيۡكَ مِنَ ٱلۡكِتَٰبِ
وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَۖ إِنَّ ٱلصَّلَوٰةَ تَنۡهَىٰ عَنِ ٱلۡفَحۡشَآءِ
وَٱلۡمُنكَرِۗ وَلَذِكۡرُ ٱللَّهِ أَكۡبَرُۗ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ مَا تَصۡنَعُونَ ٤٥



**(39) Mun halakar da Qaruna – Yayin da ya yi zalunci a kan mutanen Annabi Musa- ta hanyar kife shi da gidansa. Mun halakar da Fir'auna da wazirinsa Hamana ta dulmiyarwa a cikin teku. Kuma tabbas Annabi Musa ya zo musu da ayoyi bayyanannu, masu nuni akan gaskiyarsa, amma suka yi girman kai a qasar Misra, suka qi yin imani. Kuma ba su kasance masu kuvuta daga azabarmu ta hanya tsere mana ba.**

**(40) sai muka kama kowanne daga cikin waxanda aka ambata xin nan da azabarmu mai halakarwa, A cikinsu akwai mutanen Annabi Luxu, waxanda muka aiko musu da ruwan duwatsun yunvu. Akwai mutanen Annabi Salihu da Annabi Shu'aibu, waxanda tsawa da kama su. Akwai Qaruna wanda muka kife shi da gidansa a cikin qasa. Akwai mutanen Annabi Nuhu, da Fir'auna da Hamana, waxanda muka halaka su da nutsarwa a cikin ruwa. Da xai Allah bai kasance wanda zai zalunce su ba, ta hanyar halakar da su ba tare da wani zunubi ba, sai dai sun kasance suna zaluntar kawunansu, ta hanyar aikata savo, don haka sai suka cancanci azaba.**

**(41) Misalin Mushirikai waxanda suka xauki gumaka koma bayan Allah a matsayin abubuwan bauta, suna bauta musu don fatan su amfane su, su cece su, kamar Gizogizo ne wanda ya yi gidan da zai kare shi daga ta'addaci. Haqiqa mafi raunin gida shi ne gida Gizogizo, domin ba ya tunkuxe maqiyi. To haka ma gumakansu ba sa amfanarwa, ba sa cutarwa, ba sa ceto. Da Mushirikai sun san haka, da ba su xauki wasu gumaka suna bauta musu, koma bayan Allah ba.**

**(42) Haqiqa Allah ya san abin da suke bautawa koma bayansa, babu wani abin su da yake vuya a gare shi. Kuma shi ne mabuwayin da ba a galaba a kansa, mai hikima cikin halittarsa da qaddarawansa da gudanarwarsa.**

**(43) Waxannan misalai da muke bugawa ga mutane don su farkar da su, su ganar da su gaskiya kuma su shiryar da su zuwa gare ta, babu masu riskarsu ta yadda ya dace, sai masu ilimin Shari'ar Allah da hikimominsa.**

**(44) Allah ya halicci sammai da qassai da gaskiya, bai halicci su da qarya ko wasa ba. Lallai a cikin wannan halittar akwai dalili a bayyane a kan ikon Allah ga Muminai, domin su ne masu kafa hujja da halittar Allah a kan Mahalicci (S.W.T). Amma kafirai kuwa to suna wuce ta kan ayoyin Allah a cikin sasanni da halittu ba tare da sun jawo hankalinsu zuwa ga girman Allah Mahalicci da ikonsa ba.**

**(45) Ka karanta wa mutane abin da Allah ya yi maka wahayi da shi na Alqur'ani- Ya kai wannan Manzo-, Kuma ka tsayar da salla a kan siffar da ta fi kamala. Lallai sallar da aka tsayar da ita da cikakken siffofinta, tana hana mai yin ta faxawa cikin savo da munanan ayyuka, saboda abin da take haifarwa na haske a zukata, wanda yake hana aikata savo, ya shiryar zuwa ga ayyuka nagari. Kuma lallai ambaton Allah ya fi komai girma da xaukaka. Allah yana sane da abin da kuke aikatawa, babu wani abu na ayyukanku da yake vuya a gare shi, kuma da sannu zai saka muku a kan ayyukanku, in alheri ne, ku ga alheri, in sharri ne, ku ga sharri.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Muhimmancin buga misali, kamar misalin girgizo da Allah ya ambata.**
**2 - Saukar azaba kala-kala a duniya.**
**3 - Tsarkakar Allah daga zalunci.**
**4 - Maqalewa wanin Allah maqalewa ce ga mafi raunin madogara.**
**5 - Muhimmancin sallah wajen daidaita xabi'ar Mumini.**